ZUCIYA DA KWANJI 2

.1)Abdullahi ya mike ya fara ja da baya ba tare da fuskarsa ta bayyana tsoro ko shakka ba, sai da ya dangane da bango sannan ya daga mata hannu alamar sallamawa, yana kuma dariya ya ce. "Wai dukana zaki yi ne? Kawai sai ta ci kwalarsa cikin yanayi na fita hayyacin ta,fara magana da sarkewar murya. "Ai wallahi ba ka isa
ba... Na rantse ka yi kadan ka tozarta rayuwata.... In aure ka in ci me da kai....? Ni ba na sonka.... Na rantse yau sai ka sallame ni na bar gidan nan, in ba haka ba sai dai mu kashe juna ni da kai". Sun fi minti biyar a haka tana sakin maganar da ranta ya raya mata tana kuka,
sannan tana faman jijjiga shi har da duka. Ya tsaya kawai ya zuba mata ido,tun yana dariya har dariyar ta gagara..... Sai da ya. Tabbatar ba ta da niyyar ta hakura ,sannan ya yi maganinta.
Ya riko gashinta da karfi,wanda. Ya karya. Lagonta ta fara kara,ya dago kanta tana surutai
na cin fuska gare shi,kawai sai ya rufe bakinta

da

nasa. Ya kuma nuna mata shi jarumi namiji

ne,inda ya saki gashinta ya matse ta sosai cikin

gwaninta ya fara juya harshenta da nasa Ya

rufe

bakin masifa duk kokarinta ta kasa kwatar

kanta

ita da kanta sai da ta ji a ranta akwai inda

mazan suke. Numfashinsu ya sarke da na

juna,ya

daga aikawa kwakwalwarsu wani sako mai wuyar

fasara. Ya dai yi nasarar motsa duk wata

halittar

soyayyarta da ke zuciyarsa,ya gadar masa da

doki da fatan kasancewar su tare matsawar

numfashi.shaukin da ke shake numfashinsa bai

taba jin rabinsa daga wata ba....... Akwai

bambanci tsakaninta da shi,ita halin da ta sami

kanta bai wuce kwakwarewar komai a

kwakwalwarta ba. Ma'ana ya sauke farashin

masifarta da cushe mata zuciya kuma ya

sassauta mata zafinsa da kiyayyarsa da ta ke ji

a

makogwaronta,sai ya sanya mata raunin jiki da

na zuciya,yayin da kwakwalwarta ta dauki wani

aikin daban. Sai da Abdullahi ya fahimci hakan

sannan ya kyaleta,ya rungume ta tsan tsan a

jikinta,ta saki runane kukanta mai tsuma

rai,sai

ra bar shi da hawayen zafin kauna. Ya dago

kanta da rikitacciyar murya ya kira.

Sunanta,ya

fara girgiza mata kai... Bai jira ta ce wani abu

na

ya fara dauke hawayenta da halshensa,sai ya

....

Ashe bakinta,ya ja ta kujera ya zaunar sannan

ya

zauna gabanta a kasa da nasa kwallar ya fara

magana a tausashe. "Fatima kar ki wahalar da

numfashinmu,ba zamu iya rabuwa ba. Ban aure

ki don na saki ba tun kafin na dora idona a

kanki.... Ya ya kike tsammanin zan iya sakinki

bayan na ganki soyayyarki ta shige ni da zafi?

Ban taba dandanar so mai zakin naki ba fatima

ban taba jin a raina zan iya mutuwa a kan

mace

ba,sao akanki. Na kuma ji a raina ni ne zan da

ce

da mijinki ni dai ana aure domin bauta.....

Aurenmu ne zai samar da riba biyu, wato rayuwa

mai dadi, wadda kuma zata samar da lada,ki ba

ni dama mu gwada wannan sa'ar fatima,sai kin

sami kanki a aljannar da ta zarce ta gidan

Alh,don ba kudin ne kawai jin dadin rayuwa

ba,sannan ki sami Allah kin mai biyayya ga

umarnisa,amma me kika tanadar tsayawa

gaban

Allah idan kin yi zaman haramci da Alh?

Like · React · Report · May 15, 2015

Xaeenab Umar Yaqub

tnx

1 · Like · React · Report · May 15, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji 2

2) Da tana ta shesshekar kuka,sai a wannan

gabar ta tare shi. "Ina ruwanka? Ko kana da

kaso

a cikin hisabina? Idan haka ne ka fada min?"

Ya

kara zagewa da rarrashi. "Wannan hisabin mu

uku,ya shafa,da. Alama kuma zan fi kowa

tabewa

tunda ban mori komai ba a duniyar..... Koda

yake

ku ma din ba zaku mora ba, shaidan ne kawai yake rudinku,ko ba ki tuna yadda kike kin Alh a da? Sai bayan ya sake ki shaidan ya kawata miki shi, shi ma shaidan ya kara haska masa ke har kuka sami damar ture komai kuka halatta haram.

Hawaye ya bushe a idonta ta fara magana a sanyaye,sai dai klaman nata da zafi. "Ko ina son

Alh,ko bana sonsa binciko wannan ba zai amfane ka da komai ba, don kai dai bana sonka,kuma ba zan taba iya zama da kai da kai ba.... Kuma dole

ne ka sake ni idan ba haka ba sai dai cikinmu wani ya bar wa wani duniyar. "Ko a jikinsa,ya ce

mata. "Ai na shirya,ina fatan ke ma haka.... Na yi

mutuwar so ke ki yi taki,zan yi farin ciki idan za mu bar duniyar tare sai mu tashi da juna". "Allah

ya kiyaye". Ta fada da karaji. Ya tashi da sauri tare da dora yatsa a lebe,sannan ya fara yi mata

inkiya da window da kofa alamar kar makota su

jiyo ta ya ce. "Na riga ki a wajen Allah, ga shi kuma alhairin na je masa da shi ba sharri ba, fatima kar ki batawa kanki lokaci na fada miki ban aure ki don na saki ba..." Sai ta yi zuru tana

kallonsa lokacin da zuciyarta ta kai matukar kuntata. Ya rabu da ita ya sa kai ya shige dakin baccinta ya yi kwanciyarsa. Ta yi kukan,ta yi rurin har ta hakurkuratar da kanta ta nufi bandaki

ta dinga wankin bakinta, sannan ta zo ta dau hijabinta ta nufi kofa.yana jinta. Ta bude kofar

dakin ta fita tana faman kukan,ya yi dif yana sauraronta don yasan babu inda zata iya zuwa.illa kuwa sai gata a guje ta dawo ta shigo falon ta rufe. Ya koma ya kwanta yana dariya. Ta

fice karfe biyu da rabi a falo tana kuka,ta rasa ta

inda zata fara wannan rayuwar bakin cikin da kuma tunanin makomar lafiyar Alh da ya kwallafa

ransa a kanta,to ga jarrabar da Allah ya aiko musu. Babu dabara ta kwashi kafa ta tafi gidan

su wanda tafiyar ce zata to asirin abin da suka

binne idan Abdullahi ya bara.gara ma ta zauna

su

gurji juna duk wanda ya ji jiki sai ya sallama.

Sai

da karfe uku ta gota ya daina jin shesshekar

kukunta.da ya lallaba ya leko sai ya ganta kife

kan kujera bacci ya kwashe ta. Ya fito da bargo

a

hannunsa neman yadda zai gyara mata

kwanciyar ya zama jidali,dole sai bargon ya

rufe

mata ya wuce bandaki ya dauro alwala ya zo ya

gurfana gaban mai share hawaye. Sai hudu da

rabi ya dan kwanta ya runtsabaccin rabin

awa,sannan ya farka domin sallatar sallar

asuba.

Bayan ya dauro alwala ya zo ya bude fuskarta

yana yarfa mata ruwan hannunsa. Frigigit ta

bude

idanunta da suka yi jawur,ya ce mata. "To

sarkin

kuka tashi ki yi sallah,in yaso sai ki kai wa

ubangiji kara ta,ki dinga addu'a sai ki ga Allah

ya

warware miki duk wani kulli da ke cikin

zuciyarki,yanzu ina amfanin da kukan da kika

kwana kina yi jiya,ya samar miki? Da kin yi

dabara sai ki yi alwalarki ki kai wa ubangiji kara

ta.idan babu khairi a tare da ni ya canja miki

ni".

Ta yunkura ta tashi tana janye jiki.ya bita da

kallo da yanayi na nuna kulawa. "Me yasa ba ki

shiga wancan dakin kin kwanta ba, idan ba za ki

hada daki da ni ba? Sai ki takura kanki a nan

fatima?". Ta gyara zama tana zabga masa

harara,ta ce. "Ai ni na gama jin dadin

rayuwa,in

dai da kai zan yi ta. Ya yi murmushi,tukunna

tawa tare, tunda ni ba ni da rayuwa mai dadin

da

babu ke, sai kuma ka yi sa'a muka yi haduwar da

babu rabuwa". Cikin girgiza kan girmmar bacin

rai,ta ce "Allah ba zai cikawa maci amana irinka

burin ba Abdullahi...."

Like · React · Report · May 15, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji 2

3) Ya tare ta yana kallon kwayar idonta. "Da

na ci amanar wa? Ke ba ki san an ce mafi

sharrin

mutane shi ne wanda yake salwantar da

addininsa domin duniyar waninsa ba? Matsayin

na ke nan idan kuka yi tsani da ni kuka kulla

zaman haram...... Kuma da kike maganar Allah

ba zai cika min buri ba, ai ni Allah ya cika min

buri a kanki fatima,ya aura min soyayyarki

wanda

ina cike da fatan hakan. Tunda har Alh da kika

aura bisa kaddara kika yi zaman dole da shi ya

sami gurbin son da kike jin zaki iya zaman

haram

da shi,balle ni da kika zaba a matsayin

jaruminki

fatima.... Karkari ki yi boren ba ni da kudi, to ni

zan tabbatar miki kudi ba su kadai ne nasarar a

rayuwa ba". Ta yi kasake kawai tana kallonsa,

ya

ya aka yi ne yasa tsakaninta da Alh haka?

"Tashi

ki yi sallah" Ya fada lokacin da ya daidaita kan

sallayar,sannan ya tayar da kabbarar

raka'atainil

fijir.bayan ya idar ya sa kai ya fice masallaci.

Cikin sanyin jiki ta tashi wasu abubuwa na yawo

a ranta.dole ta yi taka tsan tsan da Abdullahi tunda ya san abubuwa da dama a kanta. Ta dauki shawararsa wajen kai kukanta wajeb mai duka sannan ta takure akan sallayar har ya dawo

masallaci ya same ta. Kai tsaye wardrobe ya wuce ya bude yana nazarin ciki,sannan ya fara yo

waje da kayan wankin kayan da ta shafe kwanakin ta a gidan tana sanyawa ba tare da ta nemi mai wanki ba. Ya ware wadanda suka kamata akai wanki ya kulle,sannan ya kwashi kananan kaya irin su vest da underware da su rigunan bacci zai fita da su. Fatina da ke satar kallonsa tun dazu sai ga ta tsaye. A kulule ta ce. "Ina zaka kai min kaya?" Ya tsaya yana dubanta,ya ce. "Wai gaisuwar ke nan?" A tsiwace

ta ce masa. "A matsayinka na wa zan gaishe ka?" Ya yi mata kallo da gefen ido,sannan ya ajiye kayan a gefe yana cewa. "To ko in zo in nuna miki matsayina?" Ta yi saurin komawa ta zauna tana kunkuni. "Abin da ka iya ke nan". Ya

tuntsure da dariya ya dauki kayan ya fice.

Yana

cewa. "Ashe har kin fahimci ni?" Can baya ya

zagaya ya wanke kayan tsab ya shanya sannan

ya dawo ya yi musu sassaukan karin kumallo.ya

shirya ba tare da ya tsumaye ta ba ya

nasa.takwas dai dai ya same ta a dakin bacci

tana zaune bakin gado tana faman kuka,kafin

maya yi magana ta riga shi. "Abdul ka cuce ni

wallahi,sannan ka cuce Alh wanda na tabbatar

zai yi wahala wannan bai zama sanadin tashin

hawan jininsa ba. Idan ya rasa ransa ta wannan

hanyar ka shirya zaka daki alhakin

mutuwarsa?"

Babu wata shakka ya amsa mata..... "Idan ke

da

kika yi sanadiyar jaza masa ciwon zuciyar ba ki

dauki hakkin mutuwarsa ba, ya ya kike

tsammanin ni zan dauka?

Like · React · Report · May 15, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

.4) Ai ni masoyinsa ne mai son saukaka masa

hisabi,idan mutuwar ce ta zo ina masa fatan

samun zaukin kwanciyar kabari". Sai da ta yi

nazari sannan ta amsa. "Sai ka bi a hankali don

kai ma dab nake da jona maka ciwon

zuciyar.idan

kuma ya kashe ka bai min asara ba sai dai ya yi

wa wadancan akuyoyin da ka ajiye". Ya yi

murmushi har kumatunsa suka lotsa ya ce.

"Allah

ya asuttura min nayi ciwon zuciya a kanki,shi

ma

Alh kaucewa umarnin manzo Allah (S . A. W) ya

yi yasa hanunsa ya yi turbaya, amma ni tsaye

nake da kafafauna. Kuma yarda ke daya ce

daga

kyallin duniya.don ...... Jajircr nake ba zan

salwantar da addinina da lafiyata dalilinki ba,

tunda lahira ba zaki amafane ni da komai ba.

Sannan idan na mutu na barki wani na za ki

aura.

Zata yi magana ya tare ta. "Kinga da Allah ya

isa,ni zan fita akwai abin da kike bukata?" Ta

yi

banza da shi,don haka ya iso gabanta yana

cewa.

"Bari na sami ladanki na rage miki wadananan

hawayen". Tuna yadda suka yi jiya ya sanya ta

zuabara ta mike,sai ga ta a hanunsa. Ba ta yi

wani yunkurin kwatar kai ba don ta san ba ta da

tsiri,kawai sai ta kwantar da kai a kirjinsa tana

kuka a hankali. Ya rungume ta da sassauci

alamar rarrashi yana fada mata kalamai masu

sanyaya rai. "Haba fadima hawayenki fa ba

abin

banza ba ne da zaki dinga salwantar da su a wofi

ba,kar ki ga ina sharewa kukanki na min ciwo

wallahi,ki ba ni lokaci na nuna miki irin kaunar

da

nake miki na rantse ba irin wadda za ki zuba a

kwandon shara ba ce".6) Haba sadiya ta yi masifar zuwa wuya, cikin

bala'I ta ce. "Wai duk aikin dubu biyu da dari

biyar din ne wannan kike....?" Hindatu tari

numfashinta ta ce. "Kwarai da gaske,tunda

wani

bai taba zuwa a gidanku ya bani kobon shi ba,

kuma har wajen Allah ban zama kaza ci ki goge

baki ba. Na hadiye alkhairi kuma na yi girgiza in

yi hamayya da wanda aka yi min ta silarsa".

Fuuu.... Sadiya ta ajiye kayan ta fice daga

wajen.Da sauri fatima ta tattare kayanta ta

gudu

daki don ba ta saba da masifa da hayaninya irin

wannan ba, ta kuma sha jin labarin fadan

kishiyoyi, yanzu idan sadiya ta fito da tabarya
da
me zata kwaci kanta? Hindatu ta ci gaba da
karatunta, sai ga sadiya da kudi 2500 ta watsa
mata, wadda ba ta yi ko gezau ba don tuni ta
saba da wannan bala'in na sadiya. Sadiya na
huci ta ce. "Sai ki hada ki kara kwazon aiki,don
ni a kansu ba zan sarayar da 'yancina ba".
Hindatu ta kwashe kudi ta bude tsakiyar
littafinta
ta zuba tana cewa. "To yanzu da ba ki sarayar
da
yanzcin naki ba fada min ribar da kika samu,
don
kin ki yarda ne, amma shi Allah babu ruwan
sa,ba a yi masa dole,kuma dole ki san sarki
goma ne zamani goma, abu turab ya gama
yayinki,sai dai ki rungumi sorry ki adana
tsufarki....." Ba ta jira cewar sadiya ba ta ture
kujera ta yi tafiyarta ta bar sadiya a nan
tsaye.
Fatima ta zube kaya kan kujera cikin
hawaye,da
me zata ji, da ganin duhun gidan nan da
ma'abocinsa,ko kuma bala'in wannan matar?

Kamar hindatu ta san yadda za a yi,karfe biyar saura minti goma Abdullahi ya dawo gida,ko kallon dakinsa bai yi ba ya sauke gajiyarsa a dakin fatima,wadda jin dirin motarsa ya sanya ta

rarumo hijab ta saka, sannan ta nemi guri ta zauna ta bata rai. Ko kala bai ce mata ba,bayan sallama bai kuma matsawa kansa kallonta bam ya shiga da jakar lap top dinsa dakinta, sannan ya fito ya wuce kicin ya dauko lemo ya dawo ya zauna a gajiye. Don neman ta kula shi, sai ya dauki remote ya sauya tashar da ta ke kallo zuwa

kwallon kafa. Nan ma sai ta share ta kwantar da kai jikin kujera kawai tana kallon rufin dakin da

fanka na juyawa wadda kamar tana hadawa da numfashinta, shi yasa ya sami damar hakura da kallon kwallon yana kare mata kallo. Can ya nakara da kayan wankin,ya dan tara gira ya ce, "Ba ki debo kayan nan da wuri ba ko?" Ta watsa musu harara shi da kayan,sannan ta kawar da kai a raunane ta ce. "Daya ke nan daga cikin cutar da ka yi min, wadda ba zan taba fanshewa ba. Da idanuna ba zan kalli mai mata na aura

ba,

bare har matansa su zame min matsala a

rayuwa.... Ni ba kaunar zama da mijinsu nake

ba,

amma haushi na suke ji". Kai tsye ya gano inda

gizo ya yi sakar,ya kuma san aikin sadiya ne

don

ya sha jinsu da Hindatu,kwanaki sai da suka

tashi hankali akan haka don haka ba shi da ta

cewa,ga shi kuma dole ya nemo,sai ya yi

murmushi ya ce. "Za su ji haushinki ne don kina

son mijinsu ko kuma dan mijinsu yana sonki?

Da

zaki yi dabara sai ki toshe kofar da za adinga

sanin tsakaininki da mijinki,dan ki ba wa mara

da

kunya.duk sharrin mutum dai ba sai ya ga abin

fada zai fada ba? Dan bata kaya sai na kuma

wankewa,mijinsu suka wahalar ba wani ba. Bai

ma saureta ba ya kwashe kayan ya fita ya kuma

wankewa ya shanya har da matsewa da clip,ya

kwashi kayan sadiya wadanda sun bushe ya kai

mata har dakinta ya ce. "Adana kayanki sun

bushe". Dan takaici sadiya kasa magana ta

yi,shi

kuma ko a jikinsa ya kada kai ya fice zuwa

dakin

fatima,ya yi wanka zuwa magarib ya fice

masallaci. Duk da haka ba zai rasa burgewa da

ya dorar a cikin zamansa da fatima wanda ya

fahimci ya fara ne tun daga ranar da sadiya ta

taka mata kayan shanya. Wato duk bala'in da

ke

tsakaninsu dairin yadda ta ke wulakanta shi a

dakinta agaban mutane karrama shi ta

ke,yadda

ko hindatu da sadiya sai dai su yi msu hasashen

matsala ba wai ta hanyar gani da ido ba, sannan

duk lokacin da take guri to sadiya ba ta isa keta

idon Abdullahi ta yi masa rashin kunya ba tare

da

ta shigar masa ba. Ya gama fahimtar ko kadan

ba sa jituwa ko sadiya ba ta zunguro bala'I a

tsakaninsu ba sai fatina ta zunguro yanzu su

tashi 'yar karamar fitina,Allah. Bashi idan sun

kebe ta hau masa boren ya kawo ta cikin

matansa suna nema jaza mata hawan jini.

1 · Like · React · Report · May 15, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

.7) Ranar

wata asabar fatima ke da girki,amma har karfe goma sha daya ba ta bude dakin baccinta ba,har ya gaji da kwankwasawa ya sa mata ido,ya yi zamansa a falo yana nazarce nazarce a computer. Can sai gata ta bude kofar ta fito tana

ta faman atishawa da alama sabuwar mura ce ta kamata.ta wuce kicin mintuna kamar goma sai gata da ruwan citta a cup zata kuma shigewa daki. "Fatima idonsa kan computer ba tare da ya

dube ta ba. Ta yi turus amma ta ki tankawa. Ya dago ya kalle ta, ya ce. "Fatima wai ba ki ji ba?"

Sai ta juyo ta nemi kujera ta zauna ba tare da ta

dube shi ba, ta fara kurbar ruwan cittarta fuskarta

a bace. Ya yi nazarinta a nutse sannan ya kara kyautata murya ya ce. "Wai komawa zaki yi ki kwanta ba zaki yi wanka ki karya ba? Ta shere kamar da dutse ya yi batunsa. Bai damu ba sai ya kuma dorawa. "Kin san kuwa abin da ya jaza miki murara nan ba zai wuce kunshe kanki da

kike a daki kina fama da sanyin A C da iskar fanka,amma ba kya gaurayawa da hasken rana da sassanyar isaka ba? Ta kuma sharewa,sai kawai ya tashi ya shige toilet ya hada mata ruwan wanka,sannan ya fito ya mika mata hannu ya ce. "Ba ni wannan cittar, shiga ki yi wanka". Ba ta musa masa ba ta dure cup ta mike ta shige wankan.kafin ta fito ya tanadar mata shayin tafarnunwa da zuma ya kai mata har daki sannan ya koma mata da madara peak wadda zata dusashe waurin tafarnuwar. Bayan ta shirya da kansa ya shasshafa mata man zafi a makogwaronta zuwa kirjinta, sannan ya rike hannunta ya yi kokarin kallon kwayar idonta ya ce. "Don Allah ki zo mu je ki sha hantsi kinji? Kar ki daka ta ni ki duba lafiyarki kinji?" Ta kawar da kai tana shakar hancin,da sauri ya saki hannunta ya yago tissue ya mika mata. Wannan dawainiyar da yake mata ce ta hanata yi masa musu wanda

ta ke ji kamar yana mata ne domin saihiyar
kaunar da yake mata tunda babu abin da yake
amfana daga gare ta. Ya daukar musu darduma
da ruwa da filo ya bata rikon ruwan da
tambulan,shi kuma ya dauko mata lemon citta
guda biyu suka tafi. Sun sami sadiya zaune a
daya daga cikinb kujeru da ke rumfar tana
danne
danne waya,Abdullahi ya yi mata sallama tare
da
dan zolayarta amma ta yi fuska. Ya shimfida
dardumar ya sanya filon sannan ya karbi ruwan
hannun fatima yana cewa. "Sannu da
kokari,zama
ban da kwanciya". Ta yi murmushi a kasalce ta
kwanta,ba tare da ta tayar da kanta akan filon
ba. Ya bita da kallo kafin ya yi magana ta riga
shi da taushin murya. "Ka yi hakuri don Allah.
Ya
ji sanyin maganar har cikin ransa,ina ma tare
da
sadiya ko hindatu suke wuni su kwana? Ya
zauna
yana mika mata filom yana cewa. "To na
hakura

sa filon". Ta girgiza kai,ta ce. "Zauna akai ka karanta min magazine. Kafin ya yi magana sai ga
hindatu cikin shirin fita.ta yi musu sallama tare da gaishe da abdullahi,ita kuma fatima ta gaisheta,Abdullahi ya ce. "Kin ga kuwa hindatu gaba dayanku ya kamata ace kun je ganin jariri,fadima muwadda. Matar yaya abdullahi ce
ta haihu na manta ne ban sanar da ke ba.ya kamata kuma ki je barka,ko bari zamu yi da dare
na kai ku gaba daya? Kamar gaske ta ce. "Ai tunda ba ka sanar da ni akan kari ba ka makara,Allah ya kai mu suna, hindatu ki shafo min kan baby...... Ya tare ta. "Idan na ce sai kun
je sai a yi yaya? "Sai ka aikata abin da bai kamata ba, ka. Debe ni da mura na je na shafawa
mutane". Hindatu ta ce. "Ni fa Abu Turab ko me
ka tsara ba zan fasa fitar nan ba tunda na shirya,sati biyar fa ban ga waje ba..... Haba kai har yanzu ba ka tsufa da kulle ba". Ta karasa

da

dariyar zolaya. Shi kuma ya saci kallon fatima

ya

ce. "Kina korafi akan wata daya,me wata uku

ta

ce me?" Fatima ta juya baya tana shakar

hanci,ta

ce. "Kai za a tambaya tunda kake jin zaka iya

maye min gurbin duk wani hali da aboki" "Dan

ma

yana kwatantawa". Inji hindatu cikin

raha.fatima

ta dan yi dariya kawai,shi ma abdullahi haka

yana kallon fatima da ta juya musu baya,ya ce.

"Ita ma dan ba ta sai da turaren wuta a gidan

biki ne shi yasa ba ta matsa min sai ta fita ba"

Ba ta damu da juyowa ba ta ce. "Ka dai samu

dama a kaina kawai,amma nawa uzurin ai ya

zarce na turaren wuta.na kuma zuba maka ido

nan da wata uku masu zuwa in sabuwar

amaryaka zata shigo ka barni na fita". Ya jima

kafin ya samo inda wannan maganar ta

samu,sai

can ya tuna ganinta,dan haka da kyar ya samo

abin cewa. "Ni ban san wata amaraya ba ban da

ke shekaru talatin nan gana ba watanin uku ba"
"Allah ya nuna mana". Inji hindatu da ta so katse
hirar bayan kishi ya sosa ranta.ta nufi sadiya tana cewa. "Kin ga sadiya dan Allah rabi kanwata
zata zo yau mun yi waya da ita yanzu suna bisa hanya, ni kuma na riga ba shirya ban son fasa fita,kuma da yake dama hutu zasu zo min sai kawai na ce su sauka a wajenki. Dama sadiya a wuya ta ke,neman me taba ta take ta fashe a kansaa. A wulakance ta ce. "Ni ma fita zan yi". Abdullahi ya dan kalli sadiya amma bai tanka ba,
sai fatima da ke jinsu ta ce. "Idan babu damuwa
ba sai ta zo wajena ba, Allah ya sa matara aure ce mu samu mai gidan nan ya barni mu sarara". "To addu'arki ba ta ci ba". Suka hada baki shi da
hindatu suna yi mata dariya,hindatu ta yi mata
godiya,shi kuma ya dubi fatima da muryar rarrashi ya ce. "Bari na kaita titi na samar mata

taxi". Ta amsa masa. Suka fice aka barta da

sadiya wajen ya yi dif! Kamar babu masu rai a

wajen, wannan ya ba wa fatima damar bacci

mai

nauyi saboda kasalar jiki. $ can hayaniyar

abdullahi da sadiya ta farkar da ita,Abdullahi

da

sadiya ta farkar da ita,Abdullahi na cewa.

1 · Like · React · Report · May 15, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

8) "Sadiya dama ana tambayata unguwa ranar

da za a yi ta ne da kike neman ki zage ni dan

na

hanaki fita?" A tsiwace ta ce masa. "To da

wanne

KWANJIN zaka ce sai na yi abin da kake so

alhalin kai ka take dukkan adalcin da ya

kamata

ace ka yi min? Ai babu wani dalilin da zai sa ka

ce sai na bi dokarka" Cikin alamar sikewa ya ce.

" Ai dama ke batunki ba ya wuce nan, kullum ke

an bata miki. A'a ba a yi miki adalci ba, komi

aka

yi miki ba a burge ki alhalin ke kin gaza da taki

biyayyar. Ni na rasa wamnan mugun son mulkin naki wallahi....." A kule ta katse shi da cewa.

"To

idan an yi min makauniya ce da ba zan gani ba,ko kana tsammanin gara ce ni irin hindatu wadda za mayar borar gida ta kasa damuwa? Ka ga tun da abin ya fara kawo mun irin wannan bakaken maganar kafin ka kai ga sa hannun ka dake ni..... Sallame ni, tunda ba kwai na ajiye a gidan ba, sai ma na ba wa wasu sarari su shigo idan sun ga zasu iya su zauna su haifi

kashi,idan

ba zasu iya ba su ma su ci taya". Fatima ta gaji da sauraronm wannan hayaninyar sai ga ta

zaune

tana mutsuke ido,sannan ta dubi sadiya ta ce. "To ke baiwar Allah akwai wanda ya yiwa Ubangiji rawa ya ba shi tsatso ne? Na tannatar kin san inda gadar haihuwa ake da yanzu mun cika gidan nan da ya'ya.mts! Ina mamakinki wallahi, ke babu wani mutum mai mutunci a idonki da ya fi karfin ki dagawa harshe. To tsoronki za a ji ayi miki abin da kike so? Ai duk mutumin da yake jin kowa ya tsane shi,to ya binciki kansa halinsa ne ba shi da kyau". Kawai

sai Abdullahi ya nemi guri ya zauna,ransa na yi
masa dadi. Fadima ta karbe shi fadan ya san
kuma yanzu zai mutu,don tana kulle sadiya da
takaici zata tafi ta ba shi guri. Sadiya ta kara
bala'I kamar zata cinye fatima danya. "Wai ke
ina
ruwanki? Ban yi miki kashedin kar ki kara shiga
sabgata ba? Ni iskar da ta kwaso ki ma idan ina
kaunar shakarta Allah ya tsine min...." Fatima
ta
yi saurin tare ta da rashin nuna damuwa. "Me
yasa za ki ce babu ruwana? Ki saka min miji a
gaba kin faman ci masa fuska ki ce babu ruwana.
To me ye amfanina? Idan ke ba kya so ni ina so,
saboda haka a kansa sai in da karfin ya kare,
ke
nan kina da bukatar canza tunanin,da ruwanan
har da komai nawa". Da sadiya ta rasa abin
cewa,sai ta harde hannu cikin rawar murya ta
ce.
"To daga nan ki sa shi ya sallame ni mana
tunda
da alama kamar ke ce mijin shi ne matar".
Fatima inda zaki, zama zaki yi ki ci gabna da
ganin abin da ba kya so, idan kin yi zuciya sai ki

canja halinki". Zuciyar sadiya ta tafasa ta

juya ga

Abdullahi ta ce. "Abu turab kayi min iyaka da

matar nan ko kuma ka bude baki ka sanr da ni

kai nake aure ko ita? "Allah ya ba ki hakuri".

Kalmar da ya fada mata ke nan cikin yanayin

cin

magani,sai ta yi kwafa ta kada kai ta bar

wajen.

Tana bacewa fatima ta tashi zaune tana hura

hanci,kafin ta yi magana sai ya riga ta, tare da

mika mata lemo. "Ungo sha makogwaronki ya

bude sai ki sauke taki rashin kunyar". Sai ya ba

ta dariya, dole ta koma ta kwanta dan kokarin

ta

hadiye dariyarta,ta ce. "Kai dai kawai ba ka

son

na fadi gaskiya, kuma sai na fada,ka kawo ni

cikin matanka suna koya min hayaniya,babu

gaira

babu dalilin ku dinga sa min ciwon kai. "Allah

yasa ya zame miki kaffara". Ya fada yana

hadiye

dariyarsa,sannan ya kwanta rigingine yana so

kadaita da tunanin hayoyin da zai canja

wadanda

za su kawo masa fatima a saukake. Babu jimawa

kannen hindatu uku suka zo ta jajibe su falonta

tana karrama su dai dai gwargwado,Abdullahi

ma

ya kwaso kafa ya biyo su,aka yi da shi inda ya

fake da murar da ta ke ya sanya su shiga

kicin,shi kuma ya ci gaba da more huldar arziki

da fatima tunda ba zata saka shi kwandon

shara

a gabansu ba. Ya dorar da ranar yau don har

abinci kwano daya ya ci da fatima.wanda rabin

su da hak ahar ya manta.

2 · Like · React · Report · May 15, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

9)Da azahar ya

kamo hanyar gida,domin ya kai su gidan

suna,ya

ce su tsaya zai kai su ne saboda fatima,wadda

ya ke matukar kishinta da hujjar fuskarta mai

hadari ce ga maza. Har ya zo gida yana tunanin

da yadda za ayi ya raba musu tafiyar tunda ta

ce

ba zata da su ba, sai Allah ya taimake shi ya

sami hindatu da kannenta su Rabi duk za su,

dan

haka.ya fake da cewa motar ta yi musu

kadan,idan ya kai su ya dawo ya kai fatima. Ko

rabin awa bai yi ba ya dawo ya dauke ta. "Wane

sauti zan sa miki?" Da batun da ya kau da

shirunsu ke nan bayan ya tashi motar,sai ta

juya

masa keya, yana dariya a ciki ya ce. "Kar fa in

sa

wanda raina yake so ki kalubalance ni". Yana

rufe

baki ta amsa masa. "Sa min dan'anace" Ya

tuntsure da dariya,sannan ya latsa sautin

wakar

bala anas "masoyiya ke ce tawa' yana cewa. "Ai

kin kawo kuka gidan mutuwa,kin ji inda na fi

kauri". Ta yi banza da shi ta kawar da kai,ya

dinga yi mata dan biki yana bin wakar yana

inkiya

da ita kamar ba tuki yake ba. Sai da suka gota

sahad store da ke zoo road sannan ta juyo ta

dube shi,ta ce. "Mu shiga zan sai kayan baby".

Ba tare da ya dube ta ba ya ce. "Ki ba ta

kudin".

Ta tara gira,ta ce. "Don me?" Ya bude ido ya amsa. "Dan ba ki yi shirin za ki shiga wani guri bayan gidan suna ba, in kin shirya shiga store sai

ki sanyo hijab har da nikab tun da akwai mazan da zaki dinga cin karo da su. Ta ce,"ga ni ga ka?"

Ya dage gira,yana mata wani kallo ya ce. "A matsayina na wa dinki?" Sai ta kawar da kai ta share,sannan ta nisa ta ce. "Mu koma sai ka shiga ka siyo min,babu komai...." Abdullahi ya yi gudun gara ya fada zago, domin shigarsa store din ke da wuya fatima ta hango direban Alh na tashin mota zai fita,da sauri ta ya fito shi ya taho jikinsa na bari kamar manta cewa,yanzu ba

shugabarsa ba ce. Ya rankwafa sosai ya gaishe ta,a rikice ta saurin katse gaisuwar,ta ce. "Ya ya

Alh?" Cikin ladabi ya amsa mata. "Ayya! Alh jiki

ya ki Hajiya,yau satina biyu a jamani. Ta fara karanto,'innalillahi wa inna ilaihi raji'un' a zuciyarta, fuskarta na nuna kololuwar tausayawa,Abdullahi na shirin kisan kai, abin

da

ta dora a ranta ke nan. Tana tuno Abdullahi sai

gabanta ya fadi, wanne irin zafin kai zai mata

idan ya zo ya tarar da ita da direba? Cikin

yanayin tsoron da damuwa ta ce. "Shi ke nan,

Allah ya ba shi lafiya. Idan kun yi waya ka fada

masa an karbi wayar hannuna ne shi yasa ba ma

samun gaisawa". Ta bude jaka ta debo kudi babu

ko kirga ta ba shi. Ya yi mata godiya ya

bace,yana tunanin wa wannan matar 'yar zafin

kai ta ke shakka haka? Matar da ya sani ba a sa

ta ba a hana ta, mulkin mallaka har ga wanda

ya

ajiye ta. Gaba daya ta sauya,wani mugun jin

haushin abdullahi ya mamaye mata

kirji,tsanarsa

ta ishe ta. Ta dinga jin gara ma mutuwarta da

rayuwar da ta ke a gidansa, kawai sai ta rafka

tagumi cikin hakakin bacin ra. Ya dawo ya miko

mata kayan,ta karba a fusace ta watsa baya.

Sai

kawai ya yi saroro yana kallonta,sannan ya

kada

kai ya zagaya ya shiga motar. Yadda ya ga

yanayinta sai ya sha jinin jikinsa,sai huci kawai

ta ke kamar ana taba ta fashewa zata yi. Bai yi shawara da kowa ba ya raba kansa da sauraron'masoyiya ke ce tawa'ya mayar da karatun alkur'ani cikin suratul kahf da muryar Abdullahi madarut.ya dinga bi cikin nutsuwa har suka kai babu wanda ya tankawa wani. Bayan ya faka motar sannan ya koma nazarinta,ya tabbatar kashi hamsin na daga kunci da ta ke ya zabge,ta bar huci ta koma tagumi da zubawa gilas ido fuskarta,ya ce. "Fadimatu me ya faru ne? Ko dan na hana ki shiga store? Haba fadimatu wannan ai karramawa ce gare ki shiga dan ni kuntata miki ba"m Kwallar da ta cika mata

ido ta fado,ba ta damu da dauke ta ba ta dube shi ta ce. "To wai don me ma zaka so ni ne Abdullahi? Soyayyarka gare ni karan tsaye ce a farin cikin ban taba shiryawa kaina auren miji irinka ba saboda haka rike ni da kake a matsayin

matarka zalunci ne gare ni' Ya yi shiru yana kallonta cikin damuwa da tarin hasshen abin da ya zunguro ta haka. Ya kife kai a sitiyari yana nazarin ta inda zai sha kanta.Rarrashinta zai yi ko kuna mayar da koken nata wasa zai yi kamar

yadda ya saba? Duk ciki bai ga na zaba ba saboda shi ma yau kirjinsa ya yi nauyi a kan lamarin. Kimanin mintuna biyar sannan ya dago
ya dube ta ya ce. "Fatima so ba ya shawara kafin
ya sami muhalli, sai dai ba shi ne mafi a'ala a cikin zamana da ke ba, idan ma ya yi tasiri ba zai
wuce na son tsarkake ruhinki da gangar jikinki daga abubuwanki,so ba zai yafe min ba idan na dauke hannu akan tarbiyyarki,ko kuma na sallame
ki dan na gaji da dawainiyar neman soyayarki har
ki sami damar zaman haramun da alh,kin san wani abu? Ko halali ne aurenki da Alh musulunci ya ba da damar a raba shi,saboda yadda Alh ya shagala da soyayarki,ke kuma kike amfani da wannan damar wajen dama garinki yadda ranki yake so,ko da ba ya kan turba. Kin san tsoron da nake jiye miki? Kar ki zama daga marasa rabo,kyawunki ya zan silar shigarki wuta,kin dauki
hakkin Alh a zamanki da shi, kun yi rayuwar

saki

uku,kuma kun fatalar da hakkin Allah kuna son

rayuwa cikin saba masa,na aure ki ina ta faman

dawainiya da hakuri da ke,fadima kar ki zama

daga cikin matan da ake saka mazajensu

aljana

saboda hakuri da munanan halayensu. Sin

fadima

an kagi halittar ki ne ba tare da wata manufa

ba?

Ki maida hankalin ki fa? Ita mutuwa ba sallama

ta ke ba bare ki ce kina da garantin lokacin tuba

ki kubutar da kanki,idan Allah a karbi ranki a

haka

ki ba ki da wani uzuri da zaki gabatarwa

ubangijin .......,ki sami lokaci ke da kanki ki yi

tunani,duniyar nan da kike ganinta ba ta kai

fikafikin sauro daraja ba a wajen Allah,inji

manzon Allah(S A W). Idan kyawunki ke rudinki

ki

farga fatima,ko kina raye shekaru kalilan kike

jira

ya gushe a sa'in da ido zai mutu kwalli ya kasa

tono shi,kuma akwai hadisin manzo Allah(S A

W )

da ya ce,'ka mori kuruciyarka kafin tsufanka'.

Akwai alamar maganganunsa sun shiga

kwanyarta da muhimmanci.hawayen ya tsaya

duk

ta yi wani wuri wuri da ita,ya jima yana kallonta

sannan ya kara tausasa murya,ya ce. "Fatima ki

taimakawa numfashinmu,mu zauna lafiya.... Ni

an

jarrabe ni da kaunarki..... Ba zan iya sakinki ba

fatima.... Kuma ba zan daina kaunarki....." Ya

kife

kai a sitiyari saboda hawayen da ya hana shi

magana,kawai sai ta sami kanta da binsa da

kallo,abin mamaki sai ta ji kukansa na taba

ranta,ita ma sai kwalla ta cika mata ido da

dinga

goge su suna kara dannowa tare da haifar mata

da makaki a zuci, abin ya yi mata yawa,ga

damuwar Alh ga ta Abdu

1 · Like · React · Report · May 15, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

.10) Haka ta dinga nade kwallarta tana dokin

wannan lokacin ya wuce musamman na damuwar

Abdul. Sai da ya yi edabarar goge hawayensa

tsab bayan ya dan sami sassauci a ransa,sannan ya juyo mata da murmushin karfin hali,sai ya ganta da hawaye.ya bude ido cikin murmushi na neman ba'asi sai ta kawar da kai tana goge fuskarta. "Ki yi hakuri kin ji, ba a son raina nake

bata ranki ba" Ya fada a can kasan makogwaronsa sai ta kasa hada ido da shi,ya ce. "Gyara fuskarki mu shiga". Bata musa ba ta bude

jakarta ta fara gyara fuskar.ta dawo fes kamar ba

ta yi hawaye ba,sai da ta mayar da kayan jakarta

ta rufe sannan ta ta dago ta dube shi suka hada

ido ya sakar mata murmushi,sai ta sami kanta da

ba shi rabbi,abin da kuma ya so birkita shi ke nan, tare da tabbatar masa ya ciyo wani birni a cikin zuciyarta.bai taba ganin murmushi a kuncinta tsakaninta da shi ba.... Ya shiga damuwar neman sanin abin da ya yi ya samo masa ita haka,wannan ya sa soyayyarta ta kara cika masa kirji,har sai da ta bayyana a

harshensa

ya furta mata. "Ina sonki fadima". Ta kawar

da

kai sannan ta balle murfin motar,ya yi saurin

ruko hannunta,a tausashe ya ce. "Bari na kira

maryam ta shiga da ke" Yana rike da hannunta

ya yi kiran kanwaesa maryan ta wayarsa,sannan

ya sauke ido a kanta,ya ce, "Karfe nawa zan zo

na dauke ki?" Muryarta na rawa ta ce. "Duk

santa ka shirya". Tana kokarin janye

hannunrta,

ya ki sakin hanun nata,ya ce. "Idan na bari sai

dare ban takura ki ba?" Ta gyara kai fuskarta

na

nuna damuwar son ya sakar mata hannu saboda

ta hango fitowa maryam,ya ce. "Rufo kofar

nan in

fito in bude miki kin ji?" Ba ta musa ba ta rufe

kofar har maryam ta karaso,sannan ya fito ya

bude mata,suna gaisawa da maryam dinmai cike

da murnar ganin fatima sai fara'a suke wa

juna.ya dauko kayan barkar ya ba wa maryam

cikin barkanci ya ce. "Ki kular min da mata kar

ki

sake ki barta da kadaici.yau in son filin

zuciyarta

fetal" Maryam na dariya,fatima na kawar da

kai

har suka wuce irin nishadin nasara a cikin

zuciyarsa. Ashe fatima na jin wakazi? Bai samo

lagonta ba kuwa? Ya shige mota da sauri ta

tashe ta ya bar wajen. Duk da fatima na

kasaita

da shan kamshi da yake tana da fara'a kuma

ga

ta da kyau,sai ta yi farin jini a dangin Abu

Turab,aka dinga nunata a matsayin amaryarsa

a

dangi.ita kuma ta ki nuna kosawa duk wanda

aka

nuna mata sai ta gaishe ahi dai dai matsayinsa

da shekarunsa. Maryam da sauran kannen Abu

turab din suka dinga hidima da ita,komai sai

sun

yi mata na musamman tare da jin ta fi karfin

wannan,ita kuma tana ta binsu da godiya. Ba ta

hadu da su hindatu ba sai daba da magariba da

su maryam suka yi mata rakiya dakin

maijegon,suka kara gaisawa da muwadda wato

mai jegon,tunda sun hadu da ta shiga bangaren

iyayen abu Turab. Sannan ta umarci maryam ta ba ta kayan wanda ita kanta ba tasan me ye a ciki ba,ashe kaya masu kayu da tsada har sati biyar,wannan ya sa muwadda ba ta iya hadiye mamakin ita kawai ba,sai da ta nuna wa wata yayar abdullahi haj Asma'u. "Anty kinga kayan da
amaryar Abu Turab ta kawo wa baby". Haj asma'u ta yaba ta yi godiya,abinka kuma da dangin miji,karaf sai wata kauwa a wajen abdullahi ta fara yiwa su sadiya da ke zaune yarfe. "Ke dai komai kin hada,ga kyau ga fara'a
,kyauta.wanda ya iya ya huta,kuma babu ruwanki
da cika mutane da surutu,gara ma mai abin kanshi tana bade mana". An ce kowa ya yi zagi a
kasuwa yasanm da wanda ya ke, hindatu ce ta fara amsawa da cewa. "Ban da abinki ai mikar mutum ba ta wuce tsawon hannunsa". Sadiya kuma na sako baki sai ta huce akan fatima. "Idan
ana cin baure ai ba a ton cikin sa,ni ban ga burgewa a cikin sayar da rai dan nemo suna ba.

Idan na adana wanda ya zame min wajibi na

gama aikina,ko ina tsiya ina matashin kai da

bargon da mutum zai rufa ma sai yana wujila

wujila da shi? A nan dai an zama kyandir". $

ban

da hindatu babu wanda ya san daga inda

maganar ta faro bare inda ta samar da ma'ana.

Dan haka maganar ta wuce sururuf bayan Haj

Asma'u ta tsawata,sai dai ta yi katon rauni a

zuciyar fatima.11) Ta tabbatar babu abin da ya fi kishi

ciwo,tunda komai bai wuce a canja maka fassara

a goranta maka shi ba, zuciyarta ta baci matuka

har ta dinga jin hawaye na son zubo mata a ido.

Dole ta sna neman tsari da wadannan kananan

maganganun sa sadiya wadda ko yaushe kiris ta

ke jira ta goranta mata akansa. Cikin dabara ta

mike ta bi Haj Asma'u tana cewa. "Anti bari na

zo na ga turarukan na akwai irin wadanda nake

amfanin da su,marayam ku zo mu je". Suaka

fice

ta bar wa su hindatu dakin,tana jin wata s'ida

a

ranta.ita yanzu ko ganin sadiyar bata mata rai

yake. A wajen haj Asma'u ta zabi turaruka

masu

kyau na kimanin dubu talatin,antin ta cire

mata

wani abu inda ta ce ba ta fito da kudi ba a tura

mata wani ta bayar. Tsab ta shiga cikin 'yan

uwan abu Turab ta baro su hindatu da ire iren

matan yaye da na dangi,don haka yayyen

Abdullahi da iyayensa suka dinga yabonta suna

jin dadin yadda ta ke daukarsu'yan uwanta, ba

kamar yadda sauran surukan sukan yi ba. Bayan

sallar magriba aka ce ga ke kadai kika zo". $ ta

kare da zolayarta,sai fatima ta yi dariya

kawai,ita

kuma anti da kanta ta je ta ce,ya fara kai su

sadiya,fatima na cin abinci, duk kuwa da ba

abincin ta ke ci ba. Shi da ya san dawan garin

bai wani musa ba ya hada kan su sadiya ya kai

su gida,ko kashe motar bai yi ba ya koma. Farin

cikin sa ya kura da ya ga wajen mutum goma su

rako masa fatima,har ma da yayyensa biyu,

suna

ta yiwa juna godiya tana sa su alkawarin kawo

mata ziyara. Da haka suka yi sallama ya ja

mota,maimakon ya yi baya su hau B.U K. Road

sai ya mike amin kano,dole fatima ta kau da

shirun da ya ratsa motar. "Ta ina zamu bi ne?"

Ba tare da ya dube ta ba, ya ce. "Zan ga likitana ne,kin san ina karbar magani." Ta tara gira,ta ce. "Na me?" Ya juyo ya dube ta,sannan ya mayar da kai ga titi "Na neman tsatso ko zan huta gorin ..... "Ga mamakin kanta sai ta ji kishi ya karci zucitarta,tare da tunano uwar gori sadiya,sai ta kawar da kai tana jin wancan kishin na dan gushewa,yayin da kwanyarta ke karanta mata, ai sadiya damuwa ce, gori kamar a jininta yake. Da suka karaso asibitin ya yi mata tayin ra raka shi, sai ta yi fuska ta ce. "Ka manta ba ka sako min hijab ba?" Dariya kawai ya yi ya fice ya rabu da ita, inda ta bishi da kallo, kirjinta na bugawa wannan asibitin ne na zuwanta,domin likintan ya san aikinsa, shi ya ba ta gwaggwabar gudubmowar hana mahaifarta karbar ciki lokacin da ta ke gidan Alh,ba tare da sanin Alh ba. A

lokacin duk bayan wata uku ta ke karbar allura, amma tun bayan mutuwar aurenta ta dauke kafa,don haka ta san yanzu idan ta shiga babu mamaki ya ishe ta da tambayoyi a gaban Abdullahi. Sai dai wasa! Tun tana jiran fitowar Abdullahi da kauna,har ta yi mugun gundura,da

ta duba agogon hannunta sai ta tarar goma ta wuce,ke nan ta yi zaman sama da awa daya a cikin motar. Ranta ya yi mugun baci, kawai sai ta balle murfin motar ta fito,kai tsaye ta wuce reception ta dinga bin mutane da ido,amma babu

abdullahi sai wasu ma'aikatan da ta sani ne suka

dinga kawo mata gaisuwa."Madam kwana biyu". Inji wata nos wai ita sister Rabi,fatima ta yi murmushi kawai domin babu amsar ba ta.ta kuma cewa. "Kuna da appointment ne?" Fatima ta yi saurin girgiza kai. "A'a wani yaro na rako,amma kinga ya shanya ni kawai fiye da awa

daya,ina jiransa" Sister Rabi ta bi jama'ar da kallo,ta ce. "Kuma babu shi a nan?" Fatima ta gyara kai, sister Rabi ta kuma cewa. "To ko

abdullahi ne? Shi ne ya jima tare da doctor"

Fatima ta hadiye takaicinta. A takaice ta ce.

"Shi

ne" Sister Rabi ta tafi tana cewa. "Bari na miki

magana da shi. Ba ta jima ba ta fito ta ce. "Ya

ce ki shiga". Dan babu yadda ta iya ne kawai ta

tura kofar ta shiga,ta tarar ana yiwa abdullahi

allura. Ta hau nazarin ofishin kafin su

gama,sannan ta nemi guri da zauna tana

harara

abdullahi.

4 · Like · React · Report · May 16, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

12) Dr ya koma mazauninsa cike da mamakin

ganin Fatima,kuma wai matar abdullahi ce, da

me

Abdullahi ya rako wannan sarauniyar matan?

Tu'ajjinbin ya tuke a nan. Suka gaisa tana

wani

basarwa ita a dole ba ta san shi ba, shi kuma ya

ki yarda da hakan,ya ce mata. "Ki yi hakuri ya

karbi wata allura ne, ya zauna zaman jiran

rabin

awa ya sha magani sannan ya karbi wata" Ba ta

tanka ba, kuma fuskarta ba ta bayyana

matakin

da zuciyarta ta dauka ba, ya kuma tambayarta.

"Madam kwana biyu?" Ta yi murmushi kawai

nan

ma ba ta tanka ba, idanunwanta na kan

Abdullahi,tana masa duban tuhu$a. Shi kuma

ya

ki yarda su hada ido.sai ya mayar da hankalinsa

ga likitan wanda ya fara yi masa bayani. "Za

mu

dinga haka duk bayan wata daya kai kuma

Allah

ya sa akwai madam a kusa sai a hana ido

bacci... Ina mana fatan dawainiyarmu ta zo

karshe Abdullahi". Abdullahi ya mike, ya mika

masa hannun yana cewa. "Insha'Allahu dr,na

gode fa". Sannan ya juya ya dube ta, ya yi

fuska

ya ce. "Ke kuma mene ne tunda kika shigo kike

ta

faman harara ta, yi hakuri yarintar tawa ce ta

motsa in ba ki hakura ba kuma idan mun koma

gida sai ki daki abinki." Ganin likita ya sa ta

maida abin wasa. "Abin da ka yi ai ya fice

kuruciya,dan na ce maka yaro is good ya ya za a
yi ka shanya ni fiye da awa daya? Idan akwai
abin da ya fice duka ma ba sai na yi maka ba,
ya
kamata duk gajiyar da na yi ka kwo ni nan ka
dire,a kalla yanzu na yi nisa da bacci. Ya hadiye
dariyar ketar da ke tattare da maganar da zata
fito bakinsa. "Watakila wata gajiyar ke
kiranki".
Ta yi masa duban rashin fahimta,amma sai ta
share saboda idon likita,suka yi masa sallama
suka fice, amma suna shiga mota ya biyo
abdullahi da kira ta waya. Sai ya dube ta,ya ce.
Don Allah zahara'u minti biyu na manto
maganin
aofishin Dr". A kufule ta mika masa hannu,ta
ce.
"Gulma dai kawai na dawainiya da ku. Ba ni key
din idan ka fice minti biyu na rantse sai dai ka
tarar da filin wajen". Yana dariya ya mika
mata,sannan ya falla da gudu. Dr ya rike
hannunsa fuska a rikice,ya ce. "Da gaske
fatima
matarka ce?" Fuskar abdullahi da alamun
mamaki

ya kada kai,likita ya sauke numfashi ya ce,

"A'a

tsaya kar muyi haka da warwara.ta amince zata

haihu da kai?" Da karsashi Abdullahi ya ce. "Ba

ta da zabi" Dr ya dururuce hannu alamar

jinjinawa ya ce. "To kar ka yi wasa, ina zaton

kukanmu ya zo karshe,don mahaifarta na

saurin

karbar ciki,sai dai ba ta da juriyar rike shi idan

ya

yi kwari,idan hakan ta kansace yana da wata

uku

za mu yi mata wani aiki,sannan mu bi lamarin

da

addu'a. Abdullahi barkatai suka taru a

kwanyan

Abdullahi lpkaci guda,albishir din likita da

fargabar yadda za su kwashe da yar rikicin ban

da minti biyun da ta ba shi. A gaggauce ya yiwa

likitan godiya ya fice. Ya dinga jan motar a

sannu

kamar ba dare ba, ne ma sai da ta yi magana.

"Yanzu don Allah a titin nan zamu kwana?" Ya

dan yi mata wani duba,ya ce. "Ai na ga kin gaji

ne bai kamata na fige motar ba ko? Ta yi shiru

ta
kawar da kai". "Kin san maganin gajiyar nan taki?
Muna zuwa gida ki yi wanka da ruwan mai dumi sannan ki dan ci kayan marmari ki sha zuma kofi
daya,tsab za ki ji kin wartsake. Nan ma ba ta tanka ba, har suka je gida yana nemanta da magana tana sharewa, shi kuma bai hakura ya bari ba. Suka shiga dakinta ya ajiye mata kayan da suka shigo da shi zai fice zuwa dakinsa,ita kuma zata shiga wanka. Ta kira shi ranta a dan bace.ya juyo ta ce. "Kar ka kuma shigo min da wanin bargo da filo dakin nan". Ya yi nazarinta da
kyau,amma yanayin bacin fuskarta ya sanya shi hadiye tambayarsa,ya yi mata. "Zumar zan kawo
miki?" Ba ta tanka ba ta wuce bandaki,shi kuma ya fice ya dan jima sannan ya dawo mata da zumar a kofi,ba tare da shakka ba ya ishe ta har
dakin bacci tana zaune gaban madubi daure da towel. Fuskarta ta nuna rashin jin dadin shigowarsa,sai dai bakinta bai furta ba. Ta karba

tana dan binsa da kallonm nazari,shi kuma ya

birkida tunaninta da siyasa,dan ya nuna bai

damu

da yadda ya same ta ba. Ya cire riga ya shiga

wanka a toilet din cikin dakin. Da sauri ta shirya

ta zira kayan bacci masu kauri ta dauki zumar

ta

fice falo cikin damuwa irin irin ta Alh da ta

shishigin da abdullahi ke mata yau

2 · Like · React · Report · May 16, 2015

Amierah S-Man

Amun hakuri rashin sa page 5

Like · React · Report · May 16, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

13) Da kuma na gorin sadiya,babu wanda

zata iya magani ba tare da ya gagare ta ko in ta

yi maganinsa ta cutu ba, wato ba ta da damar

magancewa Alh matsalarsa,shishigin Abdullahi

kuma makale da gorin sadiya,wanda maganin

gorin shi ne ta karbi tayin shi da shishiginshi, a

nan ne kuma ita zata cutu. Duk zakin zuma sai

dinga shanta kamar magani, har dai ta dire

kofin

ta dan kishigida a kasalce.ya fito shi ma sanye

da yalwatattun kayan bacci, kallo daya ta yi
masa ta kawar da kai,shi ne ya dora mata
ido,har
ya kada kai zuwa kicin ya yanko
lemo,abarba,kan
kana da gwanda ya dawofalon ya zauna kujera
kusa da ita ya sanya kayan marmarin tsakiyarsu
kan hannun kujerar,ya ce mata Bismillah". Ko
motsi ba ta yi ba, babu kuma alamar zata tanka
masa bare ta sa hannun.ya share ta ya ci gaba
da shan kayansa yana kallonta ta janyo
mayafin
ta dora aka, sannan ta kara kishingidawa can
gefe,ta juya masakeya. Ya dinga nazarinta
yana
tunanin inda zai kamo zarenta ta kula shi. Ya yi
gyaran murya tukunna ya ce. "Wai fadima me
ke
faruwa ne nake ganin ranki a bace?" Ta girgiza
kai kawai ba ta ce komai ba. Ya dan ja fasali
sannan ya ce. "Me yasa kika hana ni shigowa da
filo alhalin kina rufe dakunanki?" Ta juyo a
sanyaye ta dube shi, idanuwanta sun dan kada
alamar ranta a bace yake.ta ce. Sai ka dinga
shiga nan dakin ni ina shiga can, kafin Allah ya

yi

ikonsa akan mu... Mts! Ba na son kananan

magana ne, wai babu abin da ya wuce a ci maka

fuska a kansa,ai kishi bai yi ba wallahi." (Allah

ya

yiwa sadiya albarka) abin da ya yi ta

maimaitawa

ke nan a ransa,amma ya hana fuskarsa nuna

farin cikin da zuciyarsa ke yi,sai ya tara

jimamin

duniyar nan afuskarsa, sannan ya shiga

lallabata.

"Kofofin da nake ta fatan ki toshe ke nan tun

tuni,idan ba ki bayar da kofa ba mutum ma

shakkarki zai yi.yanzu me ye ma na sai mun

raba

dakin? Ko babu komai ai zamu dinga debewa

juna

kewa..." Ta yi saurin dubarsa,amma saboda

fuskarsa na bayyana jimami sai ta kawar da

kai,ta ce. "Ban iya yaudara ba" Ya amsa a

tausashe. "Dama babi ita a tsakaninmu,na

sanki

farin sani, kina furta min gaskiyar zuciyarki

saboda haka na san matsayina a wajenki, ni ma

bana boye miki dukkan abin da ke raina,ya sa ki
farin ciki ko akasin haka,ba na damuwa dan in
sin
tabbatar miki da gaskiyata,ke ma tun kina
ganin
bekena har ranki ya yarda babu cuta a
tsakanina
da ke..... Babu soyayya ya isa rike wani gidan
auren". Ta yi shiru ba ta tanka ba, kanta na
kallon kasa,kwalla duk ta cika mata ido. Ya
jima
yana kallonta. Harshensa bai bar addu'a ba,
tsawon wasu mintuna sannan ya ce. "Don Allah
ki rage sanyawa kanki damuwa fadima,duk abin
da muke. Cin karo da shi a rayuwarmu
rubutaccen al'amari ne daga ubangiji,damuwa
da
bacin ranki ko cida zuci na. Ba zai canja komai
ba. Nan ma ta yi shiru,ya kara jimawa yana
ambaton ismullahil azam cikin ransa, sannan ya
ce. "Ki je ki kwanta ki huta,sai ki dan bar min
dan
guri kadana ma da zan sanya hakarkarina. Duka
duniyar ma nawa ta ke,duk burikan mutum
wata

rana kabari zai sami kansa". Ta mike ba tare da

ta tanka masa ba, ta wuce daki. Ya bita da kallo

cikin dukan zuciya har mintuna goma bai ji ta

murzawa kofar key ba,ya sauke ajiyar zuciya

yana hamdala ga ubangiji,shi ya san hakuri da

na

ci da addu'a sun fara rana. Biyayya ke nan mai

kai akuya dakin kura har ta yi mata tausa

1 · Like · React · Report · May 16, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

.14) A nutse cikin tsarkin zuciya ya dauro

alwala ya gabatar da nafila raka'a shida tare

da

neman daukin ubangiji a dukkan bukatunsa na

daren yau,ya mallaka masa fatima,ya takaita

masa wahalar neman soyayyarta,sannan ya ba

shi dan kansa. Da hawayensa ya dinga yiwa

ubangiji kirari yana jaddada kokensa.bayan ya

sallame ya jima zaune gurin,sannan ya hakura

ya

ninke sallaya ya shiga bandaki ya wanke baki,ya

jefa minti a baki ya tunkari dakin da karfin

gwiwa

yana ambaton Allah. Akwai alamun idonta

biyu,saboda yadda ta takure a can karshen

gadon.ta lulluba da wani bargon ta tattare masa

na kan gadon gefe guda,ya tura kofa sannan

ya

kashe gulob,kamar mai tafiya akan ruwa saboda

tsabar shauki. Ya tattare bargon da ta ware mai

ya ajiye gefe sannan ya janyo wanda ta

takura.

Sai ta motsa a firgice, ya hana zuciyarta kai

matakin karshe a firgitar bare ta dau mataki.a

rikice ya ce. 'Au fadima ba ki yi barci ba? Gajiya

ko? Bari kawai na yi miki tausa". Bai jira

amsarta

ba,ya shisshige mata ya nuna mata abin da yake

nufi.ta yi iyakar kokarinta na son ta

bijire,amma

da yake ba a sassakata da karfe ba,ga abdullahi

ya kware wajen rikita,sai ta bayar da kai bori ya

hau,musamman idan aka kirga watannin da ta

kwashe cikin kewa dan ma an halicci mace da

kawaici. Dukkansu babu wanda bai taka rawar

azo a gani ba suma da minti talatin,amma a

karshe sai ga su kace kace cikin kuka. Babu

wanda lamarin bai zo masa a bazato ba.

Abdullahi na saka ran akwai wannan

ranar,amma

bai tsammance ta cikin sauki haka ba.... Bai

kawo ta nan kusa ba.... Bai taba zaton hadin kai

gare ta kamar haka ba..... Ga kuma tsarin

likita..... Ga shi cikin yawaita ambaton Allah da

kuma neman tsarinsa daga abin ki..... Ga kuma

fadima a cikin mata sa'ida...... Kuka ma ya

zame

masa tilas dan shi yake nuna tukewar farin ciki.

Dalilin kukan fatima sun zarce nasa a yawa, sai

dai sun fi nasa nauyi sun kuma fi su tauri a rai,

dan nata ba su rabi farin ciki ba, na bakin ciki

ne

da kaico iri iri,ya ya aka yi ta sake haka ta

faru?

Ta ci amanar Alh ta dandanawa Abdullahi

zumarta,kuma matakin ne da zai hana shi

sakinta. To da wacce fuskar ma zata ci gaba da

kallonsa kuma sa wacce zata yi masa burga?

Idan ya ki sakinta ya ya shirin zuwa nan da

wata

daya da rabi? Kukanta ya tsananta sai shi ya

hakura da sheshekar nasa,ya himmatu

rarrashinta, da kalaman ban hakuri da na nuna

kauna har da wadanda bai taba tsammanin

kwakwalwarsa zata iya kirkira ba, bai samu ta tsagaita ba sai da ya tuna mata. "Fatima kin san
fa ba mu kadai ba ne a. Gidan nan, wani fa zai iya jiyo wannan kukan naki," Ta yi dif! Illa hawayenta da ya kara gudu saboda fargabar kila
sadiya ta jiyota, kuma gobe zata iya ba ta tabbas. Ya rungume ta dan kokarinsa na tsayar da hawayenta,yana ci gaba da karanta mata kalamai masu sanyi wadanda ko kadan ba su yi tasiri akanta badan hankalinta ba ya tare da shi,sai dai da yake Abdullahi jarumi ne mai hakuri
neman so da juriya sai da ya jawo hankalinta ta ba shi nutsuwarta har ta dinga jin ranta bai rasa
komai da zai iya mallakar soyayyar mace ba, idan
aka dauke ta tunda ta riga ta sadakar da nata son ga soyayyar Alh. Sai ta yi masa bacci karya tsawon lokaci yana shafa kanta zuwa bayanta,har
ta kata alamar jan numfashin dogon bacci, sannan ya rabu da ita ya tashi zaune

musamman

yana kallon fuskarta cikin kauna iri iri. Daga

karshe ya daga hannun yana rokon Allah. "Ya

ubangiji ka saukakawa wannan baiwa taka

al'amuranta,ka yi mata gafara,ka bude

zuciyarya

ta karbi gaskiya ni ma ka bani juriya a

lamuranta... Ka gafarta min tsawon kwanakin

da

zata juyo ta yi min kallon masoyinta... Ubangiji

ka albarkace nu da zuri'a ta gari....." Wannan

addu'o'I nasa suka dawo mata da hawayenta ba

tare da ta yarda ta motsa ba dan kar ya san

idonta biyu. tana kallon ya sauka gadon ya

shige

bandaki,ya fito da wankansa,karfe uku da rabi

ya

shimfida sallaya ya dubi gabas. Da ta damu da

son ta yi kuka,kawai sai ta mike ita ma ta shighe

bandakin tana wanka tana kuka har da

karamar

shesheka.

1 · Like · React · Report · May 16, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

.15) Ta rasa da ludayin da zata kamfato

wannan rayuwar da ke neman zame mata

dole,wato zama da abduk,zuciyarta ce ke son ta

yarda tsakani da Allah abdul ke sonta, sannan

ya

cika mizanin soyayyar wadda ta isa abin

kallo,bayab wannan me ya hadata da

shakkarsa?

Me ya hadata da shiga wani garari idan ya rabe

ta? Ai ba a kansa ta fara auren ki ba, amma Alh

bai taba dadata da kasa ba Bayan wadannan

tambayoyin da zaciyarta ta kasa amsawa,akwai

illolin da za su hana ta zaman auren Abdul ko

da

kuwa ta hadiye soyayyar Alh. Shekarunta

talatin

da biyu ke nan a duniya,tsawon wannan lokacin

ba ta taba dandanar zakin so ba sai watannin

da

suka wuce wanda ta ke zargin tana kaunar

Alh,duk da ranta na raya. Mata son nasa kawai

zata tsira da shi a aurensa, tunda bai dace da

muradan ta na mijin aure ba kamar yadda ta

shekara goma da auren nasa,amma dai dai

rana

guda ba ta taba farin ciki da auren ba. To yau tsautsayi ya gamo ta da auren Abdullahi wanda ya girme mata da shekara daya kacal, sai dai ya
iyawa dabi'arta kwarai! Ya mallaki kirki da kyautatawa wadda su ne makamashin samun soyayyar mace.kirkin aljihu na fatar baki na bautawa da gangar jiki na hakuri,na sadaukar da
lokaci,na nuna damuwa a cikin damuwarta,Duk abdullahi ta yarda ya mallaka wadannan duk da
bai mallaki makudai kudade ba,amma duk da wadannan ..... Shekarin nasa babba ne matukar a
zuci,tunda gashi ya ajiye mata uku yana shirin kawo ta 4. Wannan shi ne matsalar tata, wadda abin mamaki sa ta fi kona ranta fiye da na katangar da yake shirin ginawa tsakaninta da Alh,da kuma yake shirin ginawa tsakaninta da Alh,da kuma na alfarmarta da ya keta a yau da
kuma shakkat ita ce kuwa ta biye masa hankali kwance da hadin kan da sai ta rantse ba ta taba ba wa alh rabinsa ba? Tun tana kuka kamar ta

hadiye zuciyarta har ta hadiye din ta koma

hawaye,kuma ta bar tunane tunane da hasashe

hasshen da suka cika zuciyarta. Ta yi wanka ta

fito daure da towel tana ta faman ajiyar

zuciya.Ta

bude wardrobe ta dauki wasu kayan baccin ta

zagaye Abdullahi yana sallah ta fice fala.ta

saka

kayan sannan ta nemi kujera ta zauna kawai ta

zabga tagumi duk da ta yafewa tunani,amma

hawaye fa na aikinsa har toshe baki ta ke kar

kuka ya kubuce sadiya ta jiyo. Yana sallame

raka'o'in da ta fita ta bar shi yana yi ya biyo

bayanta,saboda ciwon da kukanta ke masa,me

kama da saukar narkakkiyar dalma a gyambo.

Tun da ya fito ta sanya masa ido irin kallo na

rashin hayyaci,ya zauna kujerar da ke

fuskantarta

ya zuba mata ido shi ma, amma shi da nasa

hayyacin,sai dai zuciyarsa a dame ta ke kwarai

da tashin hankali. Ya san wannan tagumin ta yi

shi ne kawai amma zuciyarta ba ta aiki bare ace

tunani ta ke,ke nan yana bukatar dawo da ita

doka da oda tukunna idan ma rarashi zai yi ya

sami shiga. Ya koma ahannun kujerar da ta ke

zaune ya dafa kafadarta,ya ce. . "Fatima kina
son
yanke kauna da rahamar ubangiji ko,ko kuma
kina son karfi wajen cimma burikan ki?" Ta
dago
kai ta bi shi da kallo,sannan ta sauke numfashi
ta shiga goge hawayenta wanda ta ke son
tilastawa kanta tsayar da su,ko don kara su ci
gaba da tafiya a banza,lokacin amfaninsu bai
zo
ba dan tana ji a jikinta in dai zata rayu da
auren
Abdul,to an budewa rayuwarta kuntataccen
shafi.
Ganin ya sami hankalinta,sai ya dora cikin
hawaye. "Na yi nadamar abin da ya fari da mu
yau ba tare da na nemi aminciwarki hakika
ba,na
yarda abin da na yi bai kamata ba, amma ina
rokon afuwan in Allah ya so ba za ki kara
kamani
da laifi iron wannan ba..... Na miki wannan
alkawarin dan ki san ba shi kadai ne makasudin
aurena da ke ba,akwai fatan zamowarki uwar
iyalan da zan yi alfahari da su manzon Allah(S

A

W) ya yi alfahari da mu gaba daya,kin ga ke

nan

kamata na fi nema daga gare ki ba. Gara na

nemi

amanincinki da yardarki na zamowa iyalina don

ta

wannan hanyar ne wadannan zasu saukaka gare

mu.... Dan haka nake nadama,kuma ba zan

fasa

neman afuwanki ba fadina..... Idan ma ba ki

gamsu ba zan iya janye jikina daga shigowa

dakinki har sai kin yi min izin-,....

3 · Like · React · Report · May 16, 2015

Maimuna Idrees Matawalle

Tnx

1 · Like · React · Report · May 16, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

16) Sai a wannan lokacin ta kara dubansa

tana hawaye ,ta ce. "Don Allah abdul ba ka ji a

ranka ka zalunce ni ba......?" Ya yi saurin tare

ta

yana gyada kai. "Na ji.... Tabbas na ji!" Ta

koma

yi masa kallon zargi da tuhuma,ta ce. "Amma
ka
san da haka kake son ci gaba da rike ni cikin
zalunci har kake kirarin mayar da ni kamar
wadda
aka rataye,kewa da gorin matanka ya kashe ni
ko. "Zan yi hakan ne da zabinki, kuma idan har
zai faranta miki rai ko da zai bakanta min". Ta
fara gyada kai cikin sartun hawaye. "Idan
haka ne
kana son farin cikin na sallama ni kawai,shi ne
kadai abin da zai faranta min rai.ina zargin
kuma
ba zaka kalubalamce ni da komai ba,ka dora min
idda ko? Yanzu ina da damar da zan yi zaman
halali da Alh?" Ya yi saratro yana kallonta,har
ta
fitar da rai zai ce wani abu,ta dora. "Abdul don
me zaka yaudare ni? Idan ka san ba zaka
yaudare ni? Idan ka san ba zaka iya aurena ka
saki ba, don me ba ka sallame Alh da tayin
aurena da ya yi maka ba? Ban taba tsarawa
kaina miji irinka ba wallahi... Ni ban iya
hayaniya
ba ban iya bakat magana ba...kusan shekarunmu

daya,kai babu haihuwa ni babu.... Da me zamu ji?

Ta ina zamu yi tarbiyar da 'ya'yan da kake mafarki?... Ko ta ina ba mu dace da Abdul,ka dubi girman Allah ka sallame ni na tafi inda na fi

wayo inda zan iya rayuwar da na saba.... Kar ka zama me son kai Abdul,Alh ya fi ka bukatata..... Ba shi da kowa bai san son kowa ba sai nawa".

Ya yi saurin rufe mata bakinta da tafin hannunsa,

ya ja ta ya rungume,tsawon lokaci sannan cikin rawar murya ya ce. "Ina da kishi fa fatima,ina hadiye iyakar abin da zan hadiye cikin yi miki kawaici akan Alh, saboda haka kar ki kara ambaton sunansa a gabana,kin ji?

1 · Like · React · Report · May 16, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

17) Ya yi saurin rufe bakinta da tafin hannuwansa, ya ja ta ya rungume,tsawon lokaci sannan cikin rawar murya ya ce. "Ina da kishi fa

fatima,na hadiye iyakar abin da zan hadiye cikin

yi miki kawaici akan Alh, saboda haka kar ki kara
ambaton sunansa a gabana,kin ji?". Sai ta sami kanta da kasa tanak masa. Suka dauki lokaci a haka,sannan ya dagota yana kallon kwayar idonta. "Fatima,ki rabu da zaciya da sakokinta,sai
ta saka miki dubu babu alkhairi a cikin daya, lura
da ita duk abin da ta raya miki idan babu Allah a
cikinsa ki watsar kawai,ki daina barin shaidan na
wasa da zuciyarki,shi ne ya raya miki yanzu na dora miki idda kin halatta miki auren Alh? Kin jahilci hukuncin da ya haramta miki auren Alh fatima, manzon Allah (S A W) ya tsinewa mai halattawa da wanda aka alattawa,ko kin manta na san da wannan a tsakaninmu? Da na yi miki shiru sai ya kuma yi miki wasu sakokin. Ba ki iya hayaniya ba... Shekarunmu ba ki shirya auren mutum irinan....... Ashe mutumin da ba shi da wani garanti a rayuwarsa wadannan hujjojin sun
ishe uzuri? Dama yadda ka tsara rayuwa kake

samunta? Ina tsammanin ke za ki fi bayar da wannan shaidar dan tun kina budurwa kike shiryawa kanki mijin aure. Ga shi shekarunki sun

fara nisawa amma ba ki cimma wannan burin ba, me ya hana?". Suka dauki shiru tana jin nauyin

nasiharsa cikin ranta,ba ta ga laifinsa ba, amma

ta fara tsanar kanta da kaicon yadda ta ke samun rayuwa. Ya lura tana son komawa kuka sai ya dora da cewa. "Ki dan buda min filin a zuciyarki kadan yawan shekarunmu daya wani abin kaye ne a cikin soyayyarmu har nake ji a raina kamar hakan na kara min gardin soyayyarki,

wadanda ke sa hasashe kala kala masu yiwuwa da wadanda zasu yiwu ba.na ji raina da ace mutum na da ikon da rayuwarsa,tabbas da na jira

wannan lokacin na fi koshi taf! A cikin soyayyarki,zan fi gamasar da ke irin son da nake

miki, sannan ni ma zan fi gamsuwa da farin cikin

kasancewa tare da ke ko yaushe. Duk da haka zan yi kokari na kwatanta rokona da ke kawai ki bire katangar debe kaunan a tsakaninmu,insh a'Allah sai mun wadata da 'ya'yan kanmu,sauran korafe korafen ki kuma mu kai wa Allah kuka sai ya magance". Yana diga aya ta zare jikinta ta mike ta shige daki har da murza mukulli.bai nemi takura mata ba sai ya bita da kallo kawai.ya jima yana kallon kofar dakin,sannan ya sauke kai ya kishingida cikin jinjina taurin kan fatima,wadda ko kadan ba ta jin rarrashi sai dai tana da saukin jayayya. Da asuba yana dawowa masallaci ya shiga kwankwasa mata kofa yana kiran sunanta a hankali. Dole ta tashi ta bude dan kar sadiya ta sami abun fada. Tana sanye da hijabi ta zauna bakin gado ba tare da ta yarda sun hada ido ba, ya janyo stool ya zauna a gabanta yana ta faman kallonta,sai can ya kira sunanta a hankali.ta

daure ta dago kai ta kalle shi sai ta ga kwalla a idanunsa,sai kawai ta yi kasa da ido jiki a sanyaye. Ya kuma tausasa murya ya ce. "Don Allah ki yi hakuri". Ta sauke ajiyar zuciya kawai,ya kara raunana murya,ya ce. "Na fi ki damuwa fatima,don Allah ki yafe min..." Kawai sai ta sami kanta da kada masa kai idonta ya fara zubar da hawaye. Ta fara jan jiki zata tashi

ya yi saurin ruko hannunta ya yi kokarin suka hada ido,ya girgiza mata kai. "Na gode,saura ki cirewa zuciyarki damuwa ki saukakawa kanki al'amura,ki karantawa kanki dogon buri da saka karfin wajen cimmasa. Duk wani abu da yake gaibu dan adam bai isa samar da shi ta hanyar karfi da dabara ba fatima balle ya tilasta mai hukuntawa ya hukunta,Allah ba a yi masa dole fatima,kuma ba a laynace masa aikin da aka bayyanar da wanda aka boye. Saboda haka nake shawarartarki zama cikin hankalinki,ki sami lokaci

ki yi tunani mai kayu ki raba kanki da wannan kuncin,ki sake ki yi abin da aka halicce ki dominsa,wati bautar ubangiji. Sannan ki ware ki more ni'imar da ubangiji ya samar dominki,ki

bude zuciyarki farin ciki ya shiga ki rayu cikin

farin ciki da kowanduk abin da zaki so ki so shi

dai dai misali.haka ma wanda za ki ki, domin

manzon Allah (S A W) ya hore mu da rikar

al'amura tsaka tsaki. Don haka ba zan taba

matsa miki ki so ni ba, amma zan shawarceki cire

kiyayya ta daga zuciyarki saboda har kasa ta

rufe

idona babu saki a tsakanina da ke, ki kawar da

kai ga kallon ni ban cancanci kasancewa mijinki

ba, saboda ba ni da kudi duk da na yarda

neman

dai daito a aure muhimmanci abu ne, amma

aurenmu ba na shiri ba ne. Wayar kanmu kawai

muka yi cikinsa, kuma da yake ba kutatacce ne

ni

ba sai na ga kamar zan iya kwatanta

dawainiyarki,duk da ko na gaza ubangiji bai

janye

miki yi min biyayya da kayutata min ba a

matsayin bautarsa. Dukiyar nan ta ki ba zata

zama uzurinki ba, kuma ba zata cike miki

wannan

gibin ba... Kin fahimci ni? Ki kaddarawa ranki

aure na wata jarrabar ubangiji ce irin ta rashin

samun abin da rai ke so,ki yi hakuri mai kyau

Allah sai ya ba ki tarin lada kin ji?

HafsatZuciya d kwanji

18) Ya kurawa kwayar idonta ido, wadda ke

zubar da hawaye, zuciyarsa ta kara rauni,ya ja

ta

jikinsa ya fara rarrashi. Rarrashi irin wanda

babu

macen da ke juyar da shi,ya rungume ta

sannan

ya share hawayenta da harshensa tare da

sumbatarta. Tunda kwkwalwarta ba zata iya

manyan ayyuka biyu a lokaci guda ba, sai ta saki

hawayen ta karbi wannan rarrashin mai kunce

lissafi tare da nzarin makin da ya kamata ta ba

wa wannan gwarzon lakantar mace da abubuwan

da ke dauke hankalinta. Kamar masu shirin

komawa ruwa. Sai dai sun mallaki zuciyoyinsa,

muradinsu kawai su gusar da tsatsa a zuciyar

juna. Abdullahi na son nuna masa ta gamsu da

rarrashinsa,suka bata lokaci kafin su hakura da

juna,suka hada ido Abdullahi ya sakar mata

wani

murmushi sace zuciya,sai ta shanye shi ta kawar

da kai fuskarta babu yabo babu fallasa, ta ja

jikinta gado a kasalce tana jan bargo,ya saurin
sa
hannu yana taya ta, yana cewa. "Bacci ko? To
dan runtsa sai ki yi wanka ki karya,ki kwanta ki
huta sosai". Ya fara gyara dakin,sannan ya
wuce
falo.nan ma ya mayar da komai fes ya fesa
freshner ya dure kicin,ranar har wanke wanke
sai
da ya yi,samar musu karin kumallo,kana ya
shige
wanka, bayan ya fito ya tayar da ita,ita ma ta
shiga wanka. Suka karya kumallo tare kowa shiru
idan ka. Dauke sakon murmushi kauna da yake
dawainiyar jafa mata ita kuma ta hadiye ta
maze
har ya shirya ya fice bayan ya karanta mata
kalaman kauna masu zaki. Ita kuma ta koma
rudadden baccinta mai mamaye da Abdullahi
da
komai nasa,a numfashinta mafarkinta,hars
henta,kunnuwanta da dukkan iskar da ta ke
shaka,sun tura Alh wani dan sako mai kama da
kurkuku suka zagaye shi da tausayi, wanda ke
son kokawa da sabon lamarin Abdullahi wanda

zata iya kiransa fin karfin Abdullahi kawai da iya kirkinsa. ************ ********** *********** Tun daga wannan ranar bakin fatima ya mutu, ta daina kirkirar laifi domin ta bakanta masa. Ta daina ja yana ja bare su yi tanki tanka, sai dai ta dauke masa walwalarta,ta rage kazarniya kamar da,sai ya yi kwana biyu bai ji muryarta ba, iyakaci ya yi kidansa ya yi rawarsa sai ta ga dama ta kada masa kai, ko ta girgiza. Shi da kansa ya dinga yabon da dan ta kan kula shi ko da fada ne su yi, ya sami damar shigar da kansa

da fada ne su yi, ya sami damar shigar da kansa

da fada mata abin da ke cikin zuciyarsa,ko da gwasalewa ne ta yi. Bayan wannan ta kara sakar masa dawainiyar gida,ya yi hidimar waje,ya yi ta cikin gidanta,dauki ajiye ba zata yi ba, kai wanke wanken kansa sai ta daina sai ya ga haza ya wanke, girki ma idan ba ta so ba sai ya yi abincin

ta nuna bai mata ba,dole ya canja mata wani.

Ga

kuma su sadiya da tasu matsin lambar ta tutiyar

shigarsa wajen fatima ranar girkinsu da

dawainiyar da yake mata ta jiki da aljihu,duk

da

su kansu albarkacin kaza kadangare na samun

damar shan ruwan kasko,amma da yake ba haka

aka so ba, wai kanin miji ya fi miji kyau,sai

hidimarsa ba ta burge su komai ma ya yi sai a

gwasale,ban da kanana maganganu suka dinga

yi

masa yajin tsakar gida da na daki, ke nan duk

inda ya dafa babu dadi. Amma da yake

soyayyarsa na kan sharafinta take tare da

fatima

sai ya zabi soyayarta da kyautata mata kawai ko

da ba zata mayar masa raddi ba, shi babban

tashin hankalinsa ma bai fice na lafiyar da ta yi

mata karanci ba tsawon watan ni biyu ke nan,

yau zazzabi,gobe ciwon kai,jibi na ciki, kullum

matsaloli sababbi. Ya yi kuma juyin duniya ya

kai

ta asibiti ta nuna masa ta yanke gita har ranar

mutuwarta. Ya san duk cikin muntukus din da

ta

ke masa ne wato ta kashe kanta ta bar masa

duniyar. Ko yanzu zai iya dorar da auren

kyakkyawar mace da dawainiyarta wadda ta

bambanta da sauran mata,sai dai bai debe

kauna

ba. Yana saka ran akwai nasara da zai girbi ribar

abin da ya shuka. Wata rana ya tashi da

zazzabi,hindatu na ta fama da dawainiyarsa

kasancewar a dakinta yake, amma shi

hankalinsa

na kan mai ciyar masa da fatima da yi mata

sauran hidimominta. Bayan ya karya da kyar ya

sha magani ya dan kwanta yana cike da fatan

idan ya farka ya dan ji ya ware ya je ya yi

hidimar fatima,amma fatansa bai ci ba sai ma

abin da ya karu. Cikin wannan magagin ya samo

shawara inda ya umarci hindatu kira masa

malam a wayarsa. Wayar na shiga ta mika masa,

bayan sun gaisa malam ya yi masa jaje saboda

ya ji canji a muryarsa,Abdullahi ya ce. "Malam

don Allah ka taimaka min ka ba mu aron

maryam

ta karasa mana hutun a nan, dan ta dinga

taimakon fatima da 'yan ayyukan gida saboda

ita

ma ba ta da lafiya,yanzu ma muka dawo asibiti

gaba daya. Malam ya ce da shi. "Assha! Me ya

same ta ita kuma?" Sai da abdullahi ya ja

fasali

sannan ya shara karya. "Faduwa ta yi a

abndaki

ta buge kafada". Malam ya jajanta sannan ya

ce". "Babu komai,ka yiwa maryam din waya ka

ce

ta taho in ji ni, dan ba na gida a halin

yanzu,kuma sai dare zan koma". Abdullahi ya

yi

godiya,suka yi sallama ya yi fuska ya kira

maryam ya ce mata. "Kin ga maryan kome kike

yanzu ki ajiye ki hado kayanki ki taho nan, na

tambaye malam ya ce na sanar miki,ki zo yanzu

don Allah akwai wata kafa da nake so ki toshe

min" Bai jira cewarta ba ya kashe wayar yana

jan

bargo dan ba ya son irin kallon da hindatu ke

masa. Ta gaji da kallonsa dole ta soke kishi da

bacin rai ta basar,ko awa daya maryam ba ta

hada ba ta karaso,yana jiyo sallamarta da

surutanta da su ya tashi zaune yana Allah Allah

ta shigo dan karya fita ya cika azarbabi. Can ya

ji shigowarta falonsa tare da su hindatu,ya

lallaba

ya fito falon,ya yi fuska ya zauna dan yasan

tsegumi da neman rigima ya kawo su sadiya,a

dai sami abin da za a yi masa korafi. Maryam na

gaishe shi tare da yi masa sannu, shi kuma

idonsa akan jakarta da ta janyo,ya ce. "Ki

sauka

wajen fatima,ba ta cika jin dadi ba ne. Ga shi

nima haka sai ki dinga taimakonta da wasu

abubuwan,ina tsammamnin yau ko karyawa ba

ta

yi ba. Tashi ki je". Da kuzarinta ta mike tana

bayyana jimami. "Allah ya sauwake,bari na

karasa". Ya koma ya kishingida yana fadin.

1 · Like · React · Report · May 16, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

.19) "Na gode maryam". Ya yi

murmushi,maryam na fita sadiya ta hau rafta

salati da innalillahi,ya yi kamar bai san tana yi

ba. Hindatu ta muskuta ta ce. "To wai me ya

hana ba ka zube mata barori ba?" Ya yi shiru

kamar ba zai tanka ba, sai kuma ya tanka din.

"Saboda ba bakuwar mallakar barorin ba ce, zai fi armashi idan ni na zama baranta". Sadiya zata yi magana Hindatu ta yi saurin tare ta dan san zata hargitsa musu gayyar,ta ce. "Kuma kamar babu riba". Ya amsa ba tare da nuna damuwa ba. "Ke ce kike ganin haka,tunda ba ke ya shafa ba. Amma dai kin san idan babu kwadayi babu dalilin da zai sa a lashi wuta? To ki ji a ranki kokari ke bude kofar da ke kulle". Kufulalliya sadiya ta kasa hadiyewa. "Babu wata riba wallahi, ita ta zo bauta amma ita ake bautawa,to wai ita ta biya sadakin ne ko kai?" Ita ma tana rufe baki ya amsa mata. "Akwai riba mana tunda ba dan ta yi wahalhulun gida na aure ta ba. Abin da na aureta dominsa na samu, don haka babu ruwana da biyan sadakinta. Bautar da nake mata idan akwai lada Allah ya ba ni....." "Idan kuma babu fa?"

Inji

Hindatu tana kallonsa,ya ce. "Allah ya sa ya zama kaffara". Sadiya ta kara kufula, ta gyara zama ta ce "Abu Turab kana zunguro maganganu fa. Dazu haka ka ce wai ita bakuwar barori ba ce,to mu ne bakin barorin ke nan? Ko ba tasan kai talaka ba ne ta aure ka? Ta sani akwai dawainiya a gidan talaka,kuma tunda ba ita kadai ba ce a cikinsa ta sani tsab dole ta zage damtse ta yi abin da sauran 'ya'yan talakawa suke yi. Kai ma kuma tilas ka dai daita mu tunda alfaharin mace shi ne gidan mijinta ba na iyayenta ba". Ya kara yin fuska. "Idan ta san ni talaka ne ta aura,ina tsammanin na fi ta sanin ba ni da wadatar da zan samar mata jin dadin da ta saba da shi. Idan kuwa babu maganar shiga hakki,na gamsar da kaina hikimata ta zabar bauta mata da karfi KWANJI dan samar da zaman lafiya a tsakaninmu,kuma kar ta tsane ni

saboda

neman ta rasa,sai dai kawai idan akwai wadda

ta

haife ni a cikinku,sai kawai ta ladabtar da ni".

Sadiya ta mike saboda kai wa bango tana cewa.

"Kan na ka kawai ka gamsar,ita dai ihu bayan

hari kake a wajenta. Ga shi nan tana son kai ka

kabari da bakin ciki,dan ma ba ka da da balle

jika,bare ta mayar da shi maraya karfi da yaji.

Tana hanyar ficewa yana ba ta raddi. "Da bakin

ciki na ajali ai da fatima ba ta tarar da ragowar

ruhina ba,naki da tuni ya mayar da ni gawa".

Babu yadda ta iya dole ta fice din, sai Hindatu

ta

bari da 'yan kame kame. "Allah Abu Turab ka

mayar da hankalinka. Ba a taka ruwa a daki

ruwa. Matsayin sadiya da fatima daya a

wajenka,bai kamata ka dinga daga hakarkari a

kanta haka ba.... Ga shi kana ta faman

numfashi". Ya saki dogon tsaki, ya ce. "Kun

damu da lalurar tawa ne hindatu? Hassadarku

ta

fi ni kima a idonku,saboda haka duk wadda ta

ce

kulle zan ce cas! In yaso daga yanzu ta yanke

ciyar da ni tunda ita ta auro ni,ke kun fara

fitina

ta wallahi,kullum magana daya ake yi ta

yagwangwanata,kun hana kanku sukuni kun

hana

ni.... Kun koya min masifa,kun koya mata......

Ita

ma Hindatu da ta ga abin ba sauki,sai kawai ta

bar masa dakin. ****** ****** ******

******** Duk

da a bakin maryam fatima ta ji labarin

zazzabin

Abdullahi ta yi dabarar hadiye rashin

saninta,sai

dai dauko mata maryam din da ya yi, ya yi wani

tasiri a zuciyarta, har ta ji wani dan sanyi.

Zuwan

maryam din ya yi mata dadi,dan tana da tarin

bukata kamar na dauke kewa,da wata hidima

tata

ta musamman da ta shafi sirri. Dan haka ta

karbi

maryam hannu biyu fiye da zaton

mutum,maryam

kuma ta canji Abdullahi inda ta dinga yi mata

hidima kan jiki kan karfi kusan fiye ma da

Abdullahi tun da ita mace ce. Kwanaki ukun da

abdullahi ya yi yana jinya,kwana daya a dakin

Hindatu,biyu a girkin fatima sai suka zame

masa

wasu kamar na sallah,ya sami hutu kuma ya

sami kusanci da hira tsakaninsa da

fatima,domin

da ta karbi girki sai ya kwashi jinyar tasa ya

tare

a can dakinta,babu halin ta daure masa

fuska,kuma dole ta dinga yi masa sannu tana

nuna masa kulawa saboda idon maryam da ke

tare da su. Da dare ma dole suka kwana daki

duk

da ta takura kanta ne akan sofa. Kwanan

sadiya

daya da karbar girki ya dawo gida da yammaci

ya

ci karo da maryam zata shiga gida,sai ya ji babu

dadi a ransa,dan malam ba ya son fitar su

maryam kamar matan aure yake kullensu,to ina

ta je? Tana yi masa sannu da zuwa yana bata

fuska da tambayarta. "Ina kika je?" Ta daga

masa ledar da ke hannunta mai dauke da

tambarin wani pharmacy,ta ce. "Anty fatima ce ta
aike ni". Ya bi. Leadar da kallo cikin rashin fahimta,ya ce. "Kika siyo mata me?" Sai ta yi dariya kawai tana cewa. "Oho! Rubuta min ta yi na zaci ma magani ne". Da sauri ya mika hannu ya karbi ledar ya zazzago abin ciki,sai numfashinsa ya nemi daukewa,ya zare ido yana kallon maryam,ya ce. "Me zata yi da pt-strip?" Fuskar maryama ta bayyana tsoro saboda rikitar da ta ganshi a ciki. Ta debo in ina tana cewa. "Ni
.... Ni wallahi ... Ban sa.... Sani ba...... Ban ma san na me ye ba". Zuciyarsa ta kara saurin bugu,numfashinsa na son shakewa.da kyar ya dake ya mika mata tare da murmushin karfin hali,ya ce. "Ungo! Kai mata". Maryam ta wuce sukuku shi kuma sai shiga gidan ma ya gagare shi gaba daya,saboda fargabar yadda zai je wa sadiya a rikice, kila wannan ya janyo su tashi dan
karamin yaki saboda rudanin da zuciyarsa ke ciki.
Fata! Fargaba! Sun hade masa waje daya kawai sai ya shige cikin motarsa ya dinga fama da

rigimarsu. Sallar magriba ta tashe shi ya wuce masallaci amsa kiran mahalicci tare da dokin kai wancan fatan nasa gare shi. Sai karfe tara ya nemi gida bayan ya sallaci sallar isha,dadewarsa a wajen bai hana shi shiga gidan a birkice ba, saboda tsannain kaunar hada ido da fatima da ya

mamaye ransa,ba kuma hada idon kawai ba har da kaunar sauke mata tambaya daya kacal wadda a ma'auni ta fi dutse dala nauyi. "A kawo

maka abinci?" Da tambayar da sadiya ta kori shirun da ke tsakaninsu ke nan, bayan ta gama cikarta da batsewa,shi kuma ya nuna halin ko'inkula.to a nan ma sai aka kuma kwatawa,domin girgiza mata kai ya yi alamar kar

ta kawo,tunda bai ga amfanin tambayar ba. Sadiya fa ta zo wuta iyaka! Ta hadiye wani katon

kullin bakin ciki,ta ce. "To wai me yasa ba zaka sallama ni gaba daya ba? Ka hada mata kawai da

kwanakin nawa,sai ka bar ni gadin dakinka kawai,tunda ba zan ce ka barni zaman 'ya'ya

ba". Ya share ta,fuskarsa a hade ya dauki remote

ya latso tashar kallon kwallo,sannan ya ajiye remote ya wuce fridge ya dauko fura ya markada

abarsa cikin matsakaicin jug ya hado da kofi ya dawo ya zauna ya fara sha hankali kwance

abinsa. Da ta kalle shi sai ranta ya kara mungun baci,kamar ta mike ta rufe shi da duka,sai ta

zabga wani katon tsaki,ta ce. "Me ye amfanin zama da makiyi don Allah? Na rantse maka

yadda kake jin ka tsane ni haka nake jin tsanarka

dan dai kawai ba zan iya sakin kaina ba ne". Nan

ma ya shanye ya ki tanka mata abin da dama ya

dinga gudu ke nan,ga shi kuma bai tsira ba, ya kasa gane wannan bala'in na sadiya wadda ke

neman so da masifa. Har ta karaci maganganun cin fuskarta bai tanka mata ba, ta fice daga falon

cikin fushi,shi kuma ta ba shi damar fita ya tunkari dakin fatima da nufin yi mata

bankwana.ita ma da nata cin kashin ya yi

kwankwasawar duniya ta share shi, dan maryam

ta yi bacci, dole ya kwashi sassanyar gwiwa ya

doshi dakin Hindatu domin yi mata tata asubar

ta

garin. A ranar bai yi bacci kirki ba saboda tsabar

fata da fargaba.ya rasa inda zai aza tunaninsa

akan farin cikin cikin fatima ko kuma a farin

cikin

yadda cikin zai iya matsanta mata zama da shi,

ko kuma idan labarin bai kasance haka ba akan

bakin cikin yadda zata iya masa wasarere da

cikin?

2 · Like · React · Report · May 16, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji 2

.20) Da ya rasa mafita sai ya zabi ta tashi kai

wa ubangiji kokensa na godiya tare da neman

dauki. $ da safe ma bai sami ganinta ba, ya

sami

shiga falon saboda maryam ta tashi har ta fara

hidimominta amma dakin uwar dakin a kulle.

Sai

ya share ya fice kawai dan ya lura da take

takenta idan ya matsa sai ta tsinka shi wajen

maryam. *****************************

******

************************************

'Innalillahi

wa inna ilaihi raji'un! Kawai fatima ke fada

tana

maimaitawa tana ja da baya da jikin jikin din

bayan ta yar da tsinken gwajin da sauri. Tana

bin

kayan gwajin da kallo tare da shafa cikinta

lokacin da ta ke ja da baya kamar su be cikin ta

ke son gudar musu ba wanda ke jikinta ba. Ta

runtse ido ta girgiza kai da karfi tana dokin

abin

da ya faru ya zama mafarki,amma hakan ba ta

samu ba sai cikin nata ne ya yi mata inkiya da

wani karamin motsi da bayar da shaida. Ta

sulale

cikin jiri zuwa kan mat shower ta zauna cikin

kuka da girgiza kai tana hadawa da

ambaton,"A'a,a'a insha'Allahu ba zai kasance

ba!" Fiye da rabin awa tana fama da kuka da

wannan sambatun,can ta mike da wani karfin

hali

kamar na dan daudun da ya kama kadangare

ta

kuma farke wata takardar ta canja tasa ta sake

wani gwajin.tana tsaye a kansa ba ta ko kifta

ido

har lokacin ya cika ta zare tsinken shi ma ta

shiga gadinsa fiye da mintuna biyar sannan ta

daga shi cikin bugun zuciya. Har yau ba ta canja

zani ba,yanzu ya fi dazu fitowa rangadadau ma

kamar ya san shakka ta ke, kawai sai ta kece da

kuka!..21)

Tun kafin biyar ta cika Abdullahi ya dawo gida a

hikimarsa ta neman dalilin da zai sami ganin

fatima,su kebe idan ma da hali ya tambaye ta

sakamakon da gwajin ya bayar. Har biyar da

Rabi

yana zaune a dakinsa sadiya ba ta leko shi ba

bare ya hutar da tata zuciyar har ya sami

damar

tafiya ganin fatima,ga shi kuma yana kyashin

binta ya rarrashe ta tunda bai ga laifin da ya yi

mata ba. A karshe kawai sai ya fada wanka ya

shirya ya zari mukullin mota ya nufi dakin

fatima.ya same ta da maryam suna cin tuwon

shinkafa miyar danyar kubewa kwano daya.

Suna

gaisawa shi kuma yana duban agogo,sannan ya

sauke ganinsa akan fatima wadda kallo daya ya yi mata ya karanto damuwa a kwayar idonta,ya ce. "Abincin dare kuke ci ko na rana?" Ta yi murmushi yake ta kawar da kai,da haka kuma ta

bar tambayar tasa ta bi ruwa, saboda makoshinta

ya toshe da haushinsa ba ta ko kaunar bude ido ta ganshi,sai maryam ce da ta ke zaton jikin da fatima ke ji ne ya hana mata magana,ita ta amsa

masa. "Na rana ne, Anti ta kasa cin komai sai tuwo". Shi ma ya gyara zama a gabansu ya watsa hannu a kwanon yana cewa. "To Anti sannu,dama yanzu shigowa nayi mu je asibiti. Daga nan sai mu mayar da maryam gida tunda ni

na sami sauki". Sai da ta ji fasali, sannan ta amsa. "Rashin son cin wani abinci sai wani, ai ina tsammanin ba cuta ba ce,ra'ayi ne kawai saboda haka ni ba zani wani asibiti na, maryam kuma ban shirya ta tafi yau ba". "Ya kai lomar tuwo uku kafin ya amsa mata ba tare da ya dube

ta ba. "Na sani,ni 'yar burum burum ce ba na

so.... Sannan malam ba ya son su maryam su yi nisa da gida, idan muna son gaba a bamu ita ai dole mu mayar da ita akan kari,amma dai in ranki
bai so hakan ba ki yi hakuri. Ya kare maganarsa da tausasa murya dan son ya ragewa zuciyarta dacin da ta ke ji. Suka yi tsit har suka gama cin abincin maryam ta nemi wanda zai kara Abdullahi
ya amsa zai kara,har fatima ta yi musu shiru,sai
da maryam na dab da shiga kicin ta dan daga murya. "Shi ma ya koshi dan kadan zaki. Zubo masa. Sannan ta bishi da harara tana cewa. "Ban
ga fa dalilin da zaka zo ka cinye min abinci ba, alhalin ga naka can". Ya kura mata ido tare da wayon kallon cikinta,dan haka ya kasa damuwa da ma'anar kyarar da ta ke masa har ta fara tsarguwa da salon kallon nasa,sai da ya ga tsarguwar tata ta yi yawa sannan ya basar yana dariya,ya ce. "Dama kina cin tuwo? Amma kwanaki can da na yi miki kika ce min ba ki san shi ba,jiya kin yi tuwo yau tuwo,mene ne dalilin?"

Sai ta juya masa keya kawai har maryam ta

fito.ya yi mata sannu da kokari,sannan ya ce.

"Ki

shirya mu tafi". Ko daya fatima ba ta so hakan

ba, dan maryam na matukar ji da ita,tana yi

mata

hidima tare da tausayawa,ko motsi ta yi sai ta yi

mata sannu,kuma ga ta da iya girki,da hidimar

yi

mata tuwo kullum ba tare da ta cika ta da

tambaya ba. Sai da maryam ta shige

daki,sannan

ta daga kai ta dan yi masa duban rahma. "Idan

kai ka ji sauki ni naji ne? In dai don ni ka kawo

ta ke nan. Ba tare da ya dube ta ba ya amsa.

"Idan ta zauna ni ne zan kuma kwantawa, dan

na

ga yanzu ne ma kike kan sharafin kina mayar

da

ni aljihun baya. Gara ta koma gidansu ni kuma

na

koma bakin aikina,idan kin ji ciwo sai ki kimtsa

halinki",. Kawai sai ta share shi, ta mike zuwa

dakinta inda ta yiwa maryam sha tara ta arziki

har da kudin dubu goma. Suka yi sallama da

ciwon rabuwa,ya tafi mayar da ita gida. Da ya
ga
take taken fatima na sanyawa kai damuwa da
neman rigima da shi sai ya watsar kai ita kawai
yana jiran ta karbi girki dan su ji dadin yinta
su
wanye. Ranar da zata karbi girki ta samo amsar
lissafinta(-) minu,ma'ana zabar zubar da cikin
kawai tun ma kafin ya fashe ya zame mata
matsala ta ko wanne bangare,wato ta bangaren
Alh da zai san ta ci amanarsa!da kuma ta
bangare Abdullahi da zai iya yi mata karan
tsayen
zubar da cikin,ko kum$a shi da danginsa da za
su hau ta yamadidin ta sami ciki. Cikin shirin
fita
ya shigar mata sanye da fararen kaya
kasancewar juma'a ce. Ya same ta zaune falo
cikin alamun tunani, amma tana ganinsa sai ta
daure fuska,shi ma sai ya dake ya dan bata
fuska
ya ce. "Me zan yi miki na karin kumallo?" Ta
dan
biyo shi da kallo tana so ta fassara
yanayinsa,sai

ya bar mata wajen kawai ya shige dakin
baccinta,har da turo kofa.ya dinga nazarin
dakin
kamar shi zai tabbatar masa da sakamakon
gwajin da ta yiwa kanta,cikin kasala ya hakura
ya hau gyara mata gadon,ya gyara dakin
tsab,sannan ya bude bandaki shi ma ya bi shi da
kallo har idonsa ya fada kan dust bin ya hango
tsinkayen nan. Ganinsu guda biyu ma ya fara ba
shi tabbas din ya yi nasara. Ya hadiye dukkan
murnarsa,ya fito falon ya same ta har yanzu
tana
wajen da ta ke. Ya gimtse fuska ya hau gyara
falon,har sai da ya kammala sannan ya kuma
dubanta. "Har yanzu ba ki yanke shawarar abin
da kike son ki ci ba?" Ta kara daure gira,ta ce.
"Kawai ka dafa min ragowar tuwon nan". Bai
tanka ba, ya wuce kicin din kawai.ta bishi da
kallo ranta na kara yi mata daci. Tana so
tilastawa kanta ganin bakinsa fiye da
yanzu,amma da ta dube shi sai abin da ke
cikinta
ya fado mata a rai.da alama zumuntarsa da
abin
cikin nata ke mata iyaka da kaiwa matakin

karshe

akiyayyarsa. Kamar yasan hakan ya ki yi mata

shisshigi, har ya gama hidimarta ya fice. Karfe

sha daya dai dai ta shirya ta baza hijabi ta

kullop

kofarta,ba ta damu da ta yi wa kowa sallama ba,

ba don suna tsakar gidan ba sun dai gaisa da

Hindatu har ta ce mata a dawo lafiya. Ta dauki

shatar adai daita sahu zuwa asibitinta, inda ta

dakatar da shi ta shige. Dr na jin cewa ita ce,

sai

da ya ji alamun tsoro da fargaba a

ransa,saboda

tausayin Abdullahi wanda ya kwallafa rai akan

samun dan kai. Ya sallami pt da ke gabansa ya

share wadanda ke kan layi.ya ce ta shigo. Suka

gaisa a gajarce kamar yadda suka saba, shi

yana

juya kujerar yana kallonta a nutse tare da

nazarin

cikin dukan ziciya.ita kuma ta yi kicin kicin tana

bin office din da kallo kamar wanda ya canja

mata.

1 · Like · React · Report · May 17, 2015

Amierah S-Man

.Zuciya d kwanji 2

22) Abin mamaki yanzu Abdullahi ya yi min wauya kuma bai sanar min cewa kina hanya ba". Ta yi saurin dubarsa kamar a rikice, amma sai muryarta ta hadiye rikitarta,ta ce. "Ya yi maka waya akan me?" Sai da ya ja fasali sannan ya canja gaskiyarsa amsar da ya kamata ya ba ta. "Ya tambaye ni izinin zuwa ku ganin game da matsalolinki. Ya sanar da min ba ki da koshin lafiya". Ta yi shiru tana janye kai a hankali,ta jima kafin ta tanka,sannan ta nisa. "Sai ga shi na

kawo kaina, sai dai kuma babu hannunsa ko yawunsa a ciki, ni ce kawai da na da yunwar lafiyar zata halaka ni nake son karya a zumin. Ya

ci gaba da kallonta kawai da alamar tambaya har

ta gaji da shan kamshinta ta fasa. "Ciki ne da ni,

amma in so ka fitar min da shi dan ba ni da bukatarsa, sai dai bana so Abdul ya san da labarin". Kallon da yake mata ba zata iya fassara

abin da zuciyarsa ke rayawa ba, amma zuciyar

tasa ta raya manyan abubuwa,ta ga kuma girman

ta'adancin fatima da zaluncinta,wadda ba ta san

kowa ba sai kanta.... Me ya yi zafi da ta ke son

mayar da zuciyar mutum mai kirki kamar

Abdullahi dai dai da bakin tunkunya? Da

tambayar da amsar sai ya hada su ya hadiye ,ya

kuma boye abin da ke zuciyarsa,cikin sakewa ya

ce. "Ayya! Me ya yi zafi? Ni kuma gani nake ko

wanne runtsi kika shiga Hajiya barin cikin sai ya

fi zubar da shi alhairi". Ta kyabe baki,ta ce. "Ban

zo maka da tarihina dan ka yi min gyara ko ka

shawarce ni ba, in wannan ne sai in nemi

malamin falsafa. Na zo maka ne akan aikinka

wanda a kansa kake zaune a wannan kujerar". Ya

jima yana wasa da biro cikin kada kai, sannan ya

sauke numfashi ya ce. "Wanne nau'in zamu yi?"

Cikin farin ciki ta ce. "Mai sauki dai, yadda wani

ba zai fahimci halin da nake ciki ba". Ya kuma

jan

fasali, sannan ya ce. "Wata nawa ne?" Har

sauri

ta ke,ta ce. "Uku". Nan ma ya jima yana juya

al'amuran cikin ransa,sannan ya janyo takarda

ya

fara rubuce rubucensa, kana ya daga kai ya

dube

ta. "Idan haka ne,ba ma bukatar gaggawa ke

nan,sai mu yi komai cikin dabara,ki yi barinki

hankali kwance, yanzu za ki karbi allura da

magunguna mu jira sati biyu sannan ki dawo mu

dora,kin gane?" Ta kada kai zuciyarta daya. Ya

shirya mata file sannan ya yi kiran nose din da

zata ji da ita. Bayan allura har jininta aka

dauka

da ta nemi ba'asi sai nos din ta ce, mata za'a yi

wani gwajin ne. Sai sha biyu da rabi ta fito

asibitin a gurguje ta shige a dai dai sahun ya ja

suka tafi. Da yake juma'a ce yana tashi aiki

biyun

nan sai ya wuce gida. Sai da ya yi duba ya kara

bincikawa amma bai ganta ba, ya fito ya zagaya

baya sai su hindatu.ya koma yana mao tsoro da

tashin hankali,kar fa fatima ta je ta zubar

masa

da ciki?" Dan dai ya tabbatar din sai ya kuma

zagayawa baya hankali a tashe,ya ce"

"Hindatu,fatima fita ta yi ne?" Cikin shariya

ta ce.

"Eh ba ta dade da fita ba ka shigo". Ya

furta,innalillahi wa'inna ilaihi raji'un a

hankali,

fuskarsa na kara bayyana damuwa da hasasshen

inda ta tafi. A rikice ya kuma duban hindatu.

"Dama ta taba fita?" Makira sadiya ta yi

saurin

amsawa. "Eh mana". Hindatu kuma ta girgiza

kai.

"Gaskiya ni ban taba ganin ranar da ta fita

ba,idan dai ba tare kuka fita ba". Ya yi kwafa

da

rangaji ya juya.bayan tafiyarsa hindati ta dubi

sadiya ta ce. "Me yasa zaki yi mata karya

sadiya?" Ta yi tsaki ta ce. "To me ye

amfaninta?

Da kin bar ni har da sharri sai na yi mata

wallahi.

Hindatu ta girgiza kai,ta ce. "Kin manta dan

sako

ne sharri, idan ka yi shi ba ka bukatar rufe kofa

dan zai dawo maka da amsa.ba na tsammani

makirci zai yi tasiri a lamarin mutanen nan

wanda

ya wuce addu'a.kina tsammamin duk tabarar

da

ta ke bai ji haushinta ba sai fitarta ba tare da

izininsa ba? Go slow ya hade wa su fatima, ba ta

sami isa gida ba sai daya da kusan rabi,lokacin

Abdullahi ya hakura da lissafinsa ya fita za shi

masallaci,sai suka yi kacibus a tsakar gida. Ya

babbake hanyar da zata wuce ransa bace! Tsoro

ya bayyana karara a idonta, don haka tayi

saurin

kawar da kai daga kallon kwayar idonsa. Ya

daka

mata tsawa ya ce. "Daga ina kike?" Ta dan ja

da

baya dan rage tazarar da ke tsakaninsu,bakinta

na rawa ta amsa masa. "Ina ka aike ni?" Kafin

ma ta dire kawo mata mari, wanda hucinsa ne

ya

sami fuskarta saboda saurin ja da baya da ta yi

hadi da dafe kunci, ta bar shi da marin iska.

Abin

ya ba ta mamaki tare da daure kai, ta dube shi

ta

ce.23)"Abdul lna tsammanin ka kai martabar da

zaka daga hannunka da sunan kai duka a

jikina?"

Ya cije lebe yana bin gidan da kallo,sannan ya

tuna akwai'yan sa ido,kawai sai ya finciki

hannunta ya ja ta dakinsa,yana rike da

hannunta

tana yunkurin kwacewa ya sa makulli ya bude

dakin,ya ja ta ciki sannan ya mayar da kofar

ya

rufe,lokaci daya kuma ya ture ta gefe kamar

dama cizonsa ta ke,sai da ta yi namijin kokari

sannan ta sami tsaywa da kafarta tana binsa da

kallo cikin tashin hankali iri iri. Ya murza hannu

yana kallonta da fuskar gargadi. "Da ace akwai

abin da ya fi duka kaskanci. Na rantse da na yi

miki shi a yau. Na tabbatar kuma ba za a zarge

ni ba dan na kaskantar da wanda ya kaskantar

da

kansa. Ta tare shi da shafakkiyar murya. "Na

yarda ni na kaskantar da kaina na aure ka,sai

dai

kar ka shiga dimunwa wannan bai isheka damar

da zaka daki fatar jikina ka zauna lafiya ba".

Ya

naushi hanunsa yana takawa a hankali ba tare

da

ya juyo ya dube ta ba da kaukkausar murya,ya

ce. "Na rantse miki duk ranar da kika kuma

sanya

kafa kika bar gidan nan sai na yi miki abin da

zaki gamsu kai kake fara kaskantar da kanka

kafin a kaskantar da kai, kawai ki rike a ranki

duk

hakurina da kawaicina ba zai taba shafar

dokata

kulle kafarki ba tare da izinina ba ki ba ni

amsar

inda na aiki ki? An fada miki ni Alh ne? $ sai

kawai ta saki baki tana kallonsa, bai ja maganar

ba ya nufi kofa ya fice bayan ya dubi agogo.

Tana layin ta biyo bayansa,ya fice abinsa ita

kuma ta bude dakinta ta shige cikin hawaye da

takaicin yadda abdullahi ya sami damarta. Babu

abin da ya yi mata ciwo irin kalamar da ya fada

mata. "Ko an fada miki ni Alh ne?" Ta wuni da

takaici da bakin ciki goma da ashirin,ga na cikin

jikinta ga na mai cikin. Hagun wani damar wani

ita kuma sadiya ta wuni da farin cikin da
rabauta
da irinsa tun ranar da aka kawo ta matsayin
amarya.. A yau ta tabbatar duk ma wata rawar
kafa da abu Turab yake akan fatima ta bogi ce,
dan duk tsaurin idon da yake mata kirari bai
taba
gwada dora hannunsa akan fatarta ba. Duk wani
kisinme kisime da sadiya ta san zai shugabantar
da ita a zuciyar abu turab ayau ta yi shi,ciki har
da daukar shawarar kisisina da kawaye suka
dade
suna ba ta tana watsarwa. Ta yi kwalliya ta kai
kala uku,tana baza idon ganin shigowarsa dan
ta
je ta fanshe nata girkin da yake kai wa fatima
idan hargitsi ya hado su. To bai shigo gidan ba
sai bayan sallar isha, kuma abin da ya kusan
buga numfashin sadiya kai tsaye dakin fatima
ya
shige. Ta dinga bulala tuarare tana safa da
marwa a tsakar dakinta,kawai sai ta jefar da
kwalba ta tunkari dakin fatima. Ya sami fuskar
fatima a kode saboda tsabar kuka,sai duk
jikinsa

ya kara sanyi,ya dinga nacin kallonta yana aika

mata sakon ban hakuri da ido,amma ta ki yarda

ta dube shi sai faman cika ta ke tana

batsewa,ya

ajiye jaka ya isa gabanta ya durkushe ya kamo

hannuyanta ya rike da sassauci,da sauti a

makogwaro ya ce. "Ki yi hakuri fadima.... Kin

ji?

Ki yi min uzuri akan yadda na rufe ido na yi

miki

ba dai dai ba. Haka Allah ya yi ni, so ko wani

KYALLI ba ya rufe min ido na kaucewa ra'ayina

wanda ba na kirkirarsa akan son zuciya,ko babu

wata a kasa ba zan iya barinki fita sasakai na

saboda kina da sura mai hatsari.... Bari na sami

ni dan karo ne kawai a cikin rayuwarki, Allah ne

dai ya sallada shugabancinki a hannuna...

Amma

na sani... Ke ma kin tabbatar min ni ba komai ba

ne a cikin rayuwarki.... Sai dai na yi mamaki da

na ji wani matsanancin kishi wanda ban taba

tsammanin an halitar wa wani bil'adama irinsa

ba lokacin da na zo na tarar ba ki cikin gidan

nan

duk kuwa da na san ni ba wata daraja nake da

ita

ba a wajen ki ....." Ya dinga kokarin kallon

fushin

fuskarta, idanunwanta na ga talabijin, ya kai

yatsanta bakinsa ya gatsa a hankali,sannan ya

hura yana son su hada ido, amma ta ki.ya

tausasa murya ya ce. "Kin janyo abin da makota

suka ji tsanainmu ko fatima? Yanzu abin da ya

fi

damuna ke nan, wato samun kofar da za a zaci

gibi a cikin son da nake miki... Kila ke ma ki ji

hakan a ranki.... Amma kamar yadda na fada

miki

laifinki irin wannan ba zan iya hadiyewa ba don

Allah kar ki kuma,kin ji? Ina kika je? Ina

fatan ba

wajen Alh kika je ba". Ta tamke gira rai a bace

ta

juyo ta dube shi, bakinta ya dinga motsi dan

canki cankin abin da zata ce masa... A karshe ta

samu kalamar ta fito da kyar. "Dama mun yi da

kai zaka yanke dangantakar da ke tsakanina

da

shi ne? To ko wajen nasa na je batawa kai lokaci

ne ka nuna damuwa a kai..." Kwankwasa kofar

da ake ya hana ta ci gaba da magana,inda suka bi kofar da kallo su duka,a hankali abdullahi ya furta. "Shigo" Sadiya ta shigo kwas kwas tana taunar cingam ta tsira daurin dankwali daurin ture
ka ga tsiya,sai zuba yauki ake. Sai da ta karaso rukunin kujerun sannan abdullahi ya zare hannayensa daga na fatima ya mike a hankali,hankalinsa na kan sadiya wadda ta saci idonsa ta watsa wa fatima harara,sannan shi kuma ta hau yi masa gwalangwaso. "Abu Turab talabijina ce ta ki yi, zo ka duba min don Allah,zaman shiru babu dadi". Yanayin yadda ta
ke ne ya daura masa kai, don wannan kwarkwasar ba dabi'arta ba ce,ita banda masifa ma ba ta iya komai ba, don haka ma ya ga sam iya yin bai mata kyau ba. Ya saci kallon fatima wadda ta yi suguri tana kallonsu,a hankali kuma
sai ta kawar da kai cikin tunani. $ "kin janyo abin
da makota suka ji kanmu ko fatima...? Wato samun kofar da za zaci gibi a cikin son da nake miki..." Yanzu ya gama yi mata wannan karatun

ga sadiya har ta fara biyawa.... Bayan takaici sadiya har mamaki ta bata,ko ta dauka daga daji
ta fito don hala ba zata gane wannan karuwancin
ba? Ita da ta ke da dangi fal! Ko wanne gida da nasa tsarin wanne irin shakiyanci ne ba ta sani ba? Bakin abdullahi na rawa yana kuma satar kallon fatima da ta dauke musu kai,ya ce. "To ban da abinki sadiya ni gayaran talabijin na iya?
Kin lalata ta kawai sai ki jita gobe na kira miki mai gyara". Laraf fatima ta shiga maganar. "Tun
da ka jiyo ta fadi haka ai ina tsammanain gyaran
naka ne,sai dai a nan ma ai kana da wani gyaran
duk da bai taka kara ya karya ba, gama da shi sai ka yi wanka na rakaka ka duba mata". Tana rufe baki sadiya ta amsa. "Haka ne,wanda ya bata dole ya gyara duk da an baro kari tun ran tubani inji hauswa". Fatima ta yi mata shiru tana
saka amsar bata,sai dai da ta tuna mai saurin

fushi bai cika cin tiba,sai ta share ta kawai,ta

dauki remote tana latsawa tana sauraron yadda

sadiya ta dage tsakaninta da Allah tana yiwa

abdullahi shagwaba, wai sai ya zo sun tafi. Ya

kuma kasa daukar mataki a kanmta,kirjin

fatima

ya dinga radadi da zogi wanda ta kasa tantance

haushi ne ko kishi? Har sai da ta kasa hadiyewa

ta hade rai ta dubi sadiya ta ce. "Baiwar Allah

nan fa ba club ba ne da za ki ishi mutane da

haninya,shi kuma ba yaron kanti ba ne da za ki

ishe shi da tayi,ina tsammanin da karanki ya

kai

tsaiko ba sai kin batawa kanki lokaci haka ba. Na

ce ki je zai zo ya gyara miki.... Kin nace,ko sai

na janye alfarmar tawa kewar ta lahanta ki?"

Zata yi magana abdullahi ya tare ta. "Kin ga

sadiya ki je don Allah,wanka kawai zan yi in zo.

1 · Like · React · Report · May 17, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji 24) Takaici ya ishe sadiya duk

da tana ganin

ko yanzu ta yi nasara,ta juya ta fita,shi kuma

ya

rasa da idon da zai dubi fatima wadda ta kara

tamke fuska.ya yi 'yan kame kamensa sannan ya
shige wanka. Bayan ya shirya ya fara shashantar
da zuwa wajen sadiya da maganar abinci,har yana gayyatarta su fita ta sami tuwo ta ci. Ba don son cin tuwo da ya mamaye ranta ba babu abin da zai hadata fita da shi, sai ta yarda, sai dai ba cikin walwalar fuska ba. "Ina maganar zuwa duba mata talabijin?" Ya dinga nazarinta yana son gane abin da ke zuciyarta,darare ya ce.

Ta kara tamke gira,ta ce. "Don me? Idan kuma kewa ce ta dame ta fa? Ka san dole akwai ciwo,mace da mijinta mata har biyu su aure matshi,ban da ta uku me haramar zuwa maimakon layin kwanaki hudu da ta ke hawa ta koma na shida.... Ka je ka rage mata kewa kawai,duk da zan dan yi muku cikas a gabana za
a yi gyaran, amma na san ko da kallon fuskarka da sauraron muryarka kawai zata iya rage wasu kewar". Da zolaya ya ce da ita. "Idan aka fasa maganganun nan naki fa tarin ma'anini ne da su". Ta kada kafada tare da dauke kai. "Na

sani,amma na san duk yadda za a fassara maka

wasu ba lallai ka fahimta ba, saboda bambancin

dabi'u da ke tsakaninmu ta dalilin jinsi". Ya

tari

inda ta mayar da kanta yana cewa. "Ni kuma

sai

na ke ji a raina na fahimce ki fiye da yadda na

fahimci tafin hannuna,duk da kawu a

fuskokinki

kin fi nacin nuna min daya". Cikin rashin

fahimta

ta ce. "Waccec?" Da sauri ya amsa mata.

"Bayyana abin da ke cikin zuciyarki, ko da

bayyanawar zata ci karo da burinki". Ta yi

kasake,sannan ta ce. "Me kake nufi?" Ya

ce,"ki

tambaye kanki yadda kike jina a ranki game da

sadiya. Ni dai irin wannan na daga cikin abin da

ke kara min karfin gwiwa a cikin soyayarki.ina ji

a

raina duk ranar da sauran fuskokinki suka

zama

'yan gida a tawa fuskar da wuya a sami namijin

da zai kai ni farin ciki". Ta jima tana

nazari,amma

ta kasa cankar inda ya dosa,kawai sai ta yi

masa

shiru,ya jima yana kallonta sannan ya ce. "Ki

tashi ki shirya kafin sannan na dawo daga duba

mata talabijin" Ta mike a kasalce tana cewa.

Jirani zaka yi na shirya,k duba mata mu wuce".

Ba ta dami kanta da wata kwalliya ba, ta baza

hijab suka fice,tiryan tiryan har dakin sadiya.

Ta

sami kujera ta harde tana kallonsu,sadiya na

satar watsa mata harara tana yiwa abdullahi

bayani cikin yanga. "Wani film nake kallo na

tashi

sallah,wai ina dawowa na kunna sai ta ki

samuwa". Ya kunna talabijin din yana cewa.

"To

ke ce ba ki da aiki sai na kallo ba dole talabijin

ta

buga ba?" Ta kara karya murya,ta ce. "To Abu

Turab ba sai da kallon mutum zai kara gane inda

duniyar ta sanya gaba ba, kai ka ga film din da

nake kallo yanzu? Labarin wata tsohuwar mace

ce ta gama cin nata zamanin kawai ta sami yaro

ta aura,kuma don zalunci ta raba shi da

matarsa

da 'ya'yansa.ta karade danginsa da kinibibi

kowa

ta mallake,shi kansa sai yadda ta so ta ke juya

shi, ga ta yarinya sabon jini a gefe,kai! Ai

zawarawa ba su yi ba wallahi". Da yake Abdullahi

ne bai gane inda tuggun yake ba a maganar

sadiya,sai ya amsa mata da gaskiayar ransa.

"To

ina ruwan so da tsufa? Sai nawa za ki ga

tsohuwa ta yi abin da yarinya ta kas,su

'yanmata

me suak sani ban da tsabar girman kai da son

iyawa,amma kwakwalwarsu girman kai da son

iyawa,amma kwakwalwarsu empty. Sadiya tana

juya idanu ta ce. "Koma dai yaya suke sun fi

daraja tun da manzon Allah(S.A.W) ya yi

umarni

a aure su. Ya kuma amsa mata. "Sai kuma kika

manta shi da bazawarar ya fara,wadda ta yi

abin

arzikin da ba a sami budurwar da ta yi abin

arzikin da ba a sami budurwar da ta yi kamarsa

ba. Gudunmowarta a tarihin muslunci gagaruma

ce. "Ai ba zaka taba hadata da matan yau ba,

masu auren mai kudi su tatse shi tas! Daga

bisani su fita su sami yaro karami su aure,su ma

yaran da rashin sanin ciwon kai sai kwadayi ya

rude su su afka,sai ka ga sun dawo a

hannu,babu

wan babu kanin, babu kuma kudin kuma babu

KWANJIN su kuma an sha da kuruciyarsu".

Abdullahi ya sunkuya yana duba yadda ta hada

wayoyin ya ke amsa mata cikin dariya. "Ai gaba

daya sun yi min dai dai,da tsohuwar da yaron.

Ai

ba a hana mace ta auri sa'an dan cikinta ba ma,

shi ma kuma an ba shi damar aure saboda

kudi,idan kwadayin ya kai shi auren tsohuwa

mai

kudi ai ba kauce hanya ya yi ba, sai ki ga ma ta

fiye masa fakiriyar budurwar da babu

kudin,babu

kuma kyan hali.yana fama da talauci yana

fama

da rashin tarbiyarta.ita kuwa tsohuwa ta san

darajarsa,ya san tata, shi ke nan ungulu ta

biya

bukata sai balbela ta tafi da farinta. Sadiya ta

yi

iyakar kulewa,dan ta yi zargin da gayya ya yaba

mata wadannan maganganun, musamman da ta
ga hankalin fatima kwance tana murmushi. A
kuntace ta ce. "Amma dai ba haka aka so ba".
Ya
ce,"wa ya fada miki? Aure fa wuce duk yadda
kike
tsammaninsa.duk tsufan mace da wahala ta
rasa
abin da zata burge wani namiji da shi,bare a yi
kirarin ya zauna da ita bisa tilas,kin jahilci
labarin
ne sadiya,amma a mata babu babba babu
yarinya,mai hikima ce kawai zata iya samun
kan
mijinta". Sadiya ta yi dif! Ranta duk ya baci.
Ganin ta yi shiru ya sanya fatima sako baki cikin
hirar tasu. "Kayya abdul! Ai duk wanda ya
rigaka
bacci dole ya riga ka tashi,kuma da kokari ake
samun daukaka ba da kake ko uba ba, amma fa
ga wanda ya gane cewa shi zaman bariki ba
gayya ba ne, kowa da kafarsa ya zo, kuma
halinsa ke janyo masa jama'a". Sai yanzu
abdul
ya fara caftar karatun,ya saki wayoyin da suka

harde yake gyarawa da fuskar damuwa,ya ce.

"Haka ne. To mu bar maganar". Sadiya ta

fashe.

"Don me za a barta,dan kar in fadi gaskiya rai

ya

yi daci? Ai duk wanda bai ji kunyar hawa jaki

ba,

to kuwa jaki ba zai ji kunyar nana shi da kasa

ba". Nan da nan abdullahi ya bata rai. Ya tsuke

ido,ya ce. "Bana son rashin mutunci fa sadiya,

dama don haka kafa da kafa kika je kika rakito

mu?" Cikin tabe fuska ta ce.

2 · Like · React · Report · May 17, 2015

Amierah S-Man

INA HANYA GOIN BACK TO KADUNA FROM ABUJA....

Like · React · Report · May 17, 2015

Amierah S-Man

.Zuciya d kwanji 2

25) "A kaddara ma haka ne, idan ba ta yi

kasadar biyo ka ba zata ji abin da ba zai wa

ranta dadi ba ne? Ko tana ganin kafata a

dakinta

da zata ganni da kai ta ce zata shiga tsakani,

kuma da zata yi min maganar zaman bariki ba

gayya ba ne,da fa ma ba a san asalin ungulu ba

sai ta yi burgar daga masar ta zo. Na ga kina

amaryaki ma shar kofar danki ma bai ishe shi

kallo ba, sai da aka shiga aka fita aka wasko

kansa shi ne yanzu za ki yi min maganar hali?

To jiya ma me ta yi bare yau, kin san auren fari

shi ne auren so,ke kuwa kin watsar da naki

ladan

sai dai ki ga ana yi.... Kin fara ganin shaida

dazu

da kuncinki ya kusa diban yatsu biyar....!"

Abdullahi ya zuba mata ido cikin bacin rai har

sai

da ta dire sannan ya kada kai, ya ce. "Shi ke

nan

sadiya,kin kyauta sai dai ki sani ba fatima kika

wulakanta ba, ni kika ci wa fuska... Fatima zo

mu

tafi." Ya yi gaba fatima ta mike tana

murmushin

yake,ta ce. "A'a ka tsaya ka gyara mata

talabijin

mana kar dukan ya yi mata yawa. Na kwace

mata miji kuma babu abin dauke kewa, sorinki

yarinya tunda kika rasa abin da zai hana yaron

mijinki daga kai ya auro tsohuwa sa'arsa,ke dai

kurunciyarki ba ta amfane ki ba wallahi,dole ki dau hakurin rungumar filo idan kina kan layi,dan ma kin ci sa'a na kulle kofar bare ki fada layin kwana shidda..... Wata kila da wata rana karfe biyun dare za ki burmo mana kofa..." Sai da abdullahi ya hada da jan fatima suka fice daga dakin suka bar sadiya da hayaninya har da ashar.

Cikin mutuwar jikin bacin rai yake,don haka babu wanda ya tanka wani har suka isa gidan abincin,suka yi odar tuwon biski da miyar taushe da farfesu tare da kayan marmari,suna ci kowa bakinsa a dinke,kafin ya ci rabin nasa har ta share nata sai fili,ta fara shan kayan marmarin cikin yanga,ya tsura mata ido cikin tunanuwa barkartai. A nutse ya ce. "Kin koshi kuwa?" Ba tare da ta dube shi ba,ta ce. "Idan ban koshi ba cewa zan yi a karo min?" Ya yi saurin girgiza kai, ya tura mata nasa. "Ki ci wannan,bari na ji da farfesun tunda ba kya ta tasa". Babu musu ta ja

farantin da kwanon miyar ta ci gaba da ci. Bai gaji da kallonta ba, ya hada da kallon nata da shan farfesun,ya zuba mata ruwa ya tura mata. "Yau ba ki ci abincin rana ba ko?" Ta yi shiru ta ci gaba da sha'aninta, shi ma farantin ta ture,a

sannan ne kuma ya jefa mata tambayar da ta makale masa makoshi,tun kwanaki da suka gabata. "Fatima me kika yi da pt-strip?" Ya ce,"wanda na gav maryam ta siyo miki kwanaki,kuma me ake yi da pt-strip?" Ta yi fuska,ta ce. "Ina tsammanin gwajin ciki ake da shi,ni kuma a ina zan sami ciki?" Ya yi dariya,ya

ce. "To fadima mace da mijinta sai a tuhumeta inda za ta sami ciki? Fadima wannan hausar ai ba ta hadu ba". Ta fara goge hannu sannanta matsi santizer tana cewa. "Masu auren shiri ke nan, ni yanzu aka ganni da pt -strip ma ba sai a

gudu ba, mu shafe wannan maganar,wajen yara zaka ga pt-strip ka nemi ba'asi sai ka bari idan mun koma gida ka saka damba,ka kai mata kwanan dan nasan ta fi ni bukatarsa". Ya cije lebe yana dariya ya kada ido,ya ce. "Da alama

kama kin fi ta himma,tunda ga shi ba a ga pt
strip a wajenta ba aka ganshi a wajenki,ko ma
mene ne ke yake shirin yi wa lamba,kuma idan
ba
ki tabbatar min an ga pt- strip wajenki ba to in
tabbatar miki yau zan saka dambar da za a
ganshi a wajenki wani makon". Ta ji batun a
jikinta,amma sai ta hadiye ta tabe baki,ta ce.
"Kamar kana da wannan himmar ka ajiye
yaran
mata shekaru rututu babu labari..." Ya tare ta
da
cewa. "To himma biyu ai ta fi daya,yanzu ba ga
shi da himmar tawa ta sami karfin gwiwar taki
ba
suna shirin bayar da mamaki har duniya ta
gani....ai ko cikin miliyan na mata dole in na
kira
ki jaruma". Ta ja kujerar saboda rasa amsar ba
shi. Ta ce "Kan ka ake ji, ni zan tafi gida". Dole
shi ma ya mike yana dariya,ya ce. "Wato ke dai
ba za a taba jan hirar arziki da ke ba ko? To za
ki yi guzurin biskin ne,ko kuma gobe kin dawo?"
Ta yi tafiyarta ta kyale shi, sai da ya sallame su
ya tarar da ita jikin mota suka yi gida yana

kwasarta da maganganu,ita kuma hankalinta

na

ga lissafin yadda zata kubuta daga tarkonsa na

sa wa cikinta ido. Sai fita cin abinci tare ya

zame

musu dabi'a,duk ranar girinta tunda ta fi son

dukkan abincin da ya danganci tuwo,shi kuma

ba

shi da sukunin girka mata, sai ya dinga jifan

tsuntsu biyu da dutse daya,wato ya samar mata

farin ciki ta hanyar ba ta abincin da ranta ke

so,

da kuma samin damar hira da ita ko zai samu ta

fasa masa cikinta dangane da abin da yake

zargi.

Shi yasa yake dokin ta karbi girki,yayin da yake

shiga damuwar abincin da zata ci duk ranar da

ba

ta da girki,dan ma ya samo dabarar siyo mata

ya

kai mata. Sai wanan ma ya zama wani kaso a

cikin abin da ke dagawa su sadiya hankali,shi

yasa wata safiyar da zata fita girki yana ta

hanzarin ya fita saboda siyowa fatima karin

kumallo,ita kuma sadiya ta kankare shi dan

tsabar neman rigima wai sai ta raka shi,ya ce.

"Sadiya wacce tsirfa za ki tsiro idan zan je gaishe su sai na tafi da ke?" Ta ce,"ina jin ai ba a kaina aka fara ba, ranar da ka kwaso fatima ka kawo min ita wai ta rako ka duba min talabijin ita ba ta yi tsirfa ba?" Dole ya hadiye ya ce. "Shi ke nan mu je". Suka fara ta dakin Hindatu,ita kanta Hindatu sai ta ga wani sabon abu, ranta ya yi mata babu dadi, musamman da yake tana da bukatu na tambayar fita da ana tambayar kudi. To ga sadiya ta tsaye mata kerere kamar wani badogariya,sai shi Abdullahin ne ya zauna har ya sanya mata albarka a abincin da ta ke ci ba tare da ta yi masa tayi ba. Hindatu ta yiwa sadiya kallo tara ahu da murya kasa kasa ta ce. "Sauda ke nan" Sannan ta mayar da kai ga abdullahi,ta ce. "Ina ta neman wayarka tun jiya ban same ka ba, sam na manta da maganar dubo Anti

siyama...." Ya yi fuska ya ce. "Tunawar yanzu
ma
ba zata amfane ki ba, tunda kin karya ka'ida".
Ta
yi dariya ta ce". "Haba Abu Turab,uwa daya
uba
daya ai ya fice wasa, hakuri zaka yi a kawar wa
da ka'idar nan kai.... Ba zan kuma ba". Ya
ce,"haka dai kullum maganarki ke nan,ni dama
tun jiya da na ga uban turaren da kika yi na
san
yau sai kin tambaye ni fita. Wai har yaushe zan
dinga maimaita a daina tambaya ta fita ranar
da
za ayi ta?" Ta kara dagewa. "Hakuri zaka yi
Abu
Turab,antu ba zata ga kyautawar mu ba, ace sai
an kwashi kwanaki zan je dubo ta...". Ya tare
ta.
"Kar ki hada ni da ita,a dawo lafiya. Ya zaro
dari
biyar ya mika mata. "Ga kudin mota". Ta shiga
juya dari biyar din tana bin aljihunsa da kallo.
"Abu Turab... To kudin da na yi maka magana
jiya fa.... Ka ce yau zaka ba ni..." "Ni da

kaina?"

Ya fada ba tare da ya jira ta ba, ya ce.

3 · Like · React · Report · May 17, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji 2

26) "Sadiya mu je". Hindatu ta biyo shi har da

gayyar ture sadiya tana yi masa magiya,sai da

ya

ce. "Idan kin yi cinikin turaren ki ara min."

Dole

ta hakura ta kyale shi cike da haushin sadiya

wadda ta tabbatar idonta ne ya hana ya bata.

Cikin magagi fatima ta bude musu kofar ta

koma

ta zauna da bacin rai,dan tana ganin kamar

gayya ce ta sa ya kwaso mata sadiya dakinta.

Ta yi kicin kicin shi kansa ko kallonsa ba ta yi

ba. Tunda ya ga haka sai ya shafa mata lafiya,

kai tsaye ya wuce kicin yana cewa. "Me za ki ci

yau?". Ta yi masa banza,sai da ya shiga kicin

din

ya fito ya kuma tambayarta,kamar dole ta

amsa.

"Ba ni da zabi". Ya dube ta da kyau,sannan ya

dubi sadiya da ta tsaye musu,ya san kuma

ganinta ne ya tunzura fatima,duk sai ya ji
haushinta ya turnuke shi,dole ya hadiye ya
kuma
wucewa kicin ya jima tsaye ya ma rasa abin da
zai yi fiye da mintuna biyar,kawai sai ya fito
yana
cewa. "Ko za ki koma baccin,bari idan na je
office
zan turo a kawo miki abinci,yanzu in na tsaya
zan makara".. Sai ta kasa tanka masa,bare
sallamar da yake mata, suka fice sadiya biye da
shi tana jin kamar ta yi fifike don farin ciki.ta
ga
ma ashe ita ta sake tun tuni ta ba su damar
shigar mata hakki. Fatima ta dauke kai daga
kallon kofar da suka fice tana cije lebe,tare da
gyada kai, cikin tunanin mafita tare da
alkawarta
wa kanta daukar mataki. Haka kuwa washegari
sadiya ta ga hanyar ya gama shirinsa yana ta
faman kunci dan kar ta sami kafar cewa zata yi
masa rakiya kamar jiya,ita kuwa ta share shi
yana mata sallama ta makale jakarsa a kirji ta
biyo shi,babu yadda zai yi da ita suka tafi
tare,don haushi Hindatu daga bakin kofa ta

sallame su, don tana bude kofa ta ganshi sadiya ko gaishe shi ba ta yi ba ta ce masa". "A dawo lafiya,Allah tsare. Ba ta ko jira cewarsa ba ta rufe

kofarta. Ya yi murmushi kawai ya kada kai, suka

doshi dakin fatima. Ya sa key din hannunsa ya bude,amma sai ya ji alamar sakata cike da mamaki ya fara kwankwasawa dan bai taba riskarta karkama masa sakata ba. Babu jimawa ta zo ta bude bayan ta tabbatar tare yake da sadiya. Ba Abdullahi da ta danawa tarkon ba, hatta sadiya sai da ta yi turus da ganin fatima a

haka, tana sanye da farar rigar bacci sol mai zubin net,iyakar rabin cinya wadda da kadan ta zarce babu saboda babu abin da bai bayyana ba a jikinta har da kalar pant din da ta ke sanye da

shi wanda shi ma yake fari. Da alamun kasala ta jagorance su cikin falon,ta yi zamanta kan kujerar

tana doguwar hamma. Da kyar Abdullahi ya gama

kokawa da numfashinsa da kwakwalwasa mai

hajijiya da shi saboda ta gano masa hakikanin
fatima da ganin da bai taba mata ba.ya samu
ya
zauna a kujerar da ke fuskantarta kamar wani
mutu mutumi. Ya kokarta ya ce. "Sannu da
bacci". Ta yi masa wani duba da wutsiyar ido,
sannan ta kawar da kai ba ta tanka ba. Ya dan
yi
kasake yana lalubar ta inda zai sami ganin
dariyarta. Ta sake dan kishingida bayan ta yi
doguwar hamma,ya ci gaba da nacin
kallonta,muryarsa na rawa yana kokarin dai
daita. "Wai duk baccin ne, yanzu kike tashi
ne?"
Ta sauke numfashi cikin yauki ta ce.
"Wallahi,kin
tashi lafiya,sadiya ya ya dawainiya?" Ta sauke
ganinta ga sadiya ke nan wadda ta yi mugun
muzanta sai kikkifta ido ta ke tana kallon
Abdullahi wanda ta ke jin ma zata iya makanta
Abdullahi yanzu ta hana shi wannan kallon
maitar da yake wa fatima, har ma ya kasa
magana sai kallon kawai,ita kuwa gimniyar ta yi
kamar ba ta san yana yi ba. "Ina ka saka min
kayan da ka wanke rannan?" Ta tambaye shi

cikin tsura masa ido fuskarta da walwala.

Bakinsa

na rawa ya ce. "Ba ki gansu ba?.... Ta tare shi

da mikewa ta nufi daki. "Ban gan su ba". Kai

tsaye ya tashi ya bita yana cewa. "Bari mu

gani."

Ya bar sadiya da gyaran murya dan ta tunatar

da

shi ya san da ita, yana shiga ya turo kofa. Har

da

murda key dan yana zaton sadiya zata biyo shi.

Sai fatima ta juyo suka fuskanci juna fuskarta

na

baYyana alamar tuhumarsa da rufe mata kofa.

Ya

kama hannayenta a rikice ya ce. "Fatima,me

yasa

kike saka irin wadannan kayan baccin ni a tare

da

ki?" Ta yi masa kallon rashin fahimta,sannan

fara

bin rigae jikinta da kallo. Ya fara yi mata

shishigi,yana cewa. "Ki dinga sanya kaya masu

kauri idan kina ke kadai dan yiwa shaidanu riga

kafi... Ko ba ki san kina da kirar da za a kalla a

kasa kawar da kai ba..? Ni kima ina da kishi

musamman a kanki,kin ji fatima. Kamar dama

bai

fada don ta amsa masa ba, ya fara sumbatarta

cikin gigita da shauki,kamar a majigi sai ta biye

masa suka bata hankalin dare matuka! Fiye da

mintuna goma sha biyar,ita kanta da ta dana

tarkon ta manta tarko ne,ta manta da sadiya

bare shi da ya fi ta zakewa. Suka samar da wasu

guraba masu muhimmanci a zukatan

juna,Abdullahi ya ba ta assigment mai zafi na

neman dalilin da ta ke kasa mallakar

kanta,idan

sun shaki numfashi juna.... Ta kasda sanin

dalilin

tana ji kuma a ranta ko rabuwa da shi zata sha

wannan kewar.... Abdul ya iya da mace ya iya

bayyana mata kauna

2 · Like · React · Report · May 17, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji 2

27) A yau ta samar wa zuciyarsa nutsuwar da

ya jima cikin damuwa da tantamar matsayinsa

a

zuciyarta, ya yarda ya sake ne shi yasa fatansa

ke nisa farin cikinsa na binsa a baya. Tabbas duk lokacin da fatima ta karbi soyayyarsa sai ya shiga sakun mazan da suka yi sa'ar auren kyawawan mata wadanda suka karanci so. Ya dago ta da riko kafardarta jiki a sanyaye.

"Fatima,kin tuna cewa cikin wata nan bakwai mu

ke da aure?..... Dadewa tare na nufin sabo da komai ma idan ta kama har da gajiya..... Amma ni har yau ban saba d sonki ba don kullum In wayar gari da wasu sababbin sonki wanda ban taba dandanar irinsu ba, saboda ganinki ba ya hana in ganin kyan fuskarki kullum,yau fiye da jiya, yadda kike mu'amalanta ta ba ta sa ni yanke

kaunar za ki shugabantar da ni cikin duniyar wata

rana ba kuma ga shi ina zama wani sabon shiga duk san da na shaki numfashinki...... Amma na san ba komai ba ne sai tsananin kaunarki da ta cakude da jinina,fadima ban taba jingina kaunarki

da wani dalili ba.... Kin amince min? Ki yarda da

ni..." Ya ci gaba da kura mata idanunwansa da

suke fitar da kwalla suke son su yi tasiri a zuciyarta su sanya ta yin abin da babu niyyarsa a burikanta, sai ta yi kasa da ido,ya dago kanta yana nuna mata agogo,a sanyaye ya ce. "Kin ga kin sani na makara fadima,duba agogo me zaki ci? To taya ni mu gyara dakin ko" Ba ta tanka. Shi ba, kuma ba ta taya shi ba, sai ma ta nufi ward robe ta dauko after dress ta maka ta yi zamanta kan sofa tana kallonsa har ya gama da dakin ya fice falo,sai can jimawa ya shigo mata. "Zan tafi fatima". Ta dago ta bi shi da kallo, ya daga gira ya ce. "Ki yi hakuri,zan turo miki break fast kamar jiya,na makara...ki yi min wannan uzurin". Sai ta sami kanta da daga masa hannu da sarkarkiyar murya,ta ce. "Babu komai ka je,ba sai ka ka turo ba zan nemi abin da zan ci". Ya yi kaske yana kallonta, murna duk ta cika masa zuciya.... Da ya rasa abin da zai ce mata sai ya debo mata sambatu. "Dama ace ke za ki karbi girki,da da wuri zan dawo na yi miki tuwo da kaina". Ta ci gaba da sa masa ido kawai har ya

gama sambatunsa ya fice. Ta mayar da kai a

hankali,tare da son fadawa cikin tunani,sai a

sannan sadiya ta fado mata,da sauri ta fito

falon

sai ta ganshi wayam! Sai Abdullahi da ke ficewa.

Ta zube a kujera cikin tsananin dariya tare da

furta. "Yarinya kin kuma kiran me alewa ba ki

da

kobo". Shi kansa Abdullahi sai a lokacin ya tuna

wai fa tare da sadiya ya shigo.dan haka a

tsorace

ya silale ya bar gidan.

1 · Like · React · Report · May 17, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji 2

.28) A

gaggauce fatima ta yi wanka zuciyarta cike da

fargabar yadda zata fita ta dawo ba tare da

Abdul

ya san da fitarta ba,ita kanta sai ta dinga

mamakin tsoron da ta ke masa, wadda ta ke jin

ba tsoron ne kawai ba har da rashin son bacin

ransa, da kuma hangen matakin da zai iya

dauka

wanda ta ke canke canke akai.da fadawa kawu

sirrinta zai fanshe ko kuma da yi mata dukan shan gishiri? Bayan wannan komai nasa ya karade zuciyarta, tana tuna shi a muhimman lokutansu,da jarumtarsa wajen bayyana mata kauna yadda ya kware wajen gigita fuskokin shaukinta, sannan ga bautar da yake mata jiki da
jini. Wadannan dalilan suka sanya ta jin kamar tana son ta ci amanarsa a yunkurin ta na zubar masa da ciki musamman a matsayinsa na me neman haihuwa ido rufe. Wannan alhini bai hana
ta shiryawa tana duban agogo ba,wanda ya nuna
sha daya da 'yan mintuna. Tana tsaye a falonta
ta jaka da mayafi a hannu,sai ga kawarta laila kuma tafinta tsakaninta da Alh a lokacin da ta ke
zaman gida. Ta yi farin ciki da ganinta sosai,suka
gaisa sannan suka zauna suna bincikar labarin juna. "Sai yau nake ganinki a gidan nan laila kin
watsar da ni kin barni ni kadai da azancina.

Abdullahi na ta samun nasarori a kaina,ina

Alh?

Laila ta dinga bin dakin da kallo cikin tabe baki,

sannan ta ce. "To in zo in yi me a wannan bakin

gidan? Ai da alkwarin na yi har ki bar shi ba zan

tsomo kafata mai daraja a cikinsa ba. To da

alama ke ba kya ganin duhunsa da

kuncinsa,tunda na ga har wata 'yar kwarya

kwaryar kiba kika yi.... Kin bar Alh na can yana

fama da jinya,to jiya ya sauka kasar nan kuma

shi ya buga sammako da kansa ya same ni har

gida ya ce lallai na zo na ji inda naki lissafin

yake,ya ya aka yi kika bace haka... Fatima ina

wayoyinki?" Fatima ta dan yi walai da ido

alamar

bayyana jimami,sannan ta nuna kofa tana

cewa

"Ya karbe". Laila ta ji batun gingirin,ta tsule

gira

ta dubi kofar sannan ta dubi fatima ta ce. "Ya

karbe?"Wanne sale dan kwadago ya samu haka

har ya sami wannan zakewar,ke kuma wuka ya

dora miki a wuya ya kwaci wayoyin ko kuma

barazana ya yi miki da bindiga cewa,in kika

kuma

wata wayar zai harbe ki? Fatima ta yi

murmushin

yake tare da sauke ajiyar zuciya mai bayayyana

gajiyar zuciya,ta ce. "Ya faki idona ya

kwashe,sannan ya toshe hanyar da zan fita

bare

in mallaki wata wayar,tsawon watannin nan

bakwai fa da muka yi tare ban yi fita ta kai

goma

ba, kuma ga kafata ga tasa,sai sati biyun da

suka

wuce na saci hanya na je asibiti, shi ma ba ki ga

dan bikin da ya yi min ba, har fa da mari...."

Labarin ya girgiza laila kwarai,ta jinjina

"Mari?"

Fuskar taki ya mara fatima? To dan ganye

ne?"

Fatima ta yi murmushi,ta ce, Ko daya idan ma

yana sha ba zai wuce giyar sona dake bugar da

shi ba. Na rantse miki na kasa gane wanda ya fi

so na tsakanin sa da Alh....." Laila ta yi saroro

kawai tana kallonta,tara gira ta ce. "Da alama

kuma kin biye masa.... Soyayyar da yake miki ba

hujja ba ce da zaki yi zaman watanni bakwai a

gidansa.... Ke ni gani nake ma tsaurin ido ne

mutumin bai fice baranki ba ya iya furta

soyayyarki". Fatima ta jima shiru tana juya

maganganun lailan,ta yarda a ranta laila ba ta

san waye Abdullahi ba,koda yake suna da

bambancin dabi'u da alkibla ita da laila.

Ma'ana

kudi sun runtse idon laila,yayin da ita ta ke son

rayuwar'yanci da rayuwa da abin da ta ke so

wanda kuma ta. Zabar wa kanta da kanta da

dalilan da ko kusa baba kudi a cikinsu. Sai ta

sami kanta da kwalla,ta dubi laila ta ce da ita.

"Ki yi farin ciki laila da Allah bai yo ki kamar ni

ba,kyan tarnaki ne a cikin rayuwa wanda mafi

yawan lokuta yake hana mutum zabar abin da

yake so ake hada shi da zabin wasu,sakamako an

yi masa shigar sauri don a rayu da shi dole! Na

tabbatar yawancin kyawawan mata ba sa auren

mazan da suka dace da burinkansu". Cikin

fuskar

rashin fahimta laila ta ce. "Me kike nufi?"

Fatima

ta yi saurin amsawa. "Ba ki ga aya a kaina ba?

Na zauna da Alh bisa kaddara ta kara hadani

da

Abdul..... Wanda nake ganin kamar ya fo Alh

zafin so na... Kamar ya fi shi sadaukarwa..."

Laila ta tare a kufule. "Idan kin zauna da Alh

bisa

dole,wallahi ba ki fadi ba zahra'_ don ya isa ya

ajiye kamarki a gidansa,sannan ya mallaki wani

abu da zai rage miki takaicin kiyayyarsa....'Udi

ai

su ne a yanzu,don haka ban ga dalilin da za ki

zauna da mai gidan nan ba, me ya ajiye,da me

ya

cancanci mallakar mace kamar ki... Da me za ki

karasa ragowar rayuwarki..." Fatima ta yi saurin

tare ta fuska a hade. "Wannan ra'ayinki kike

fada

laila, akwai muhallai da yawa wadanda ba kudi

ke taka rawa a cikinsu ba, musamman na

dadada

zuciya ba, laila ni ban fifita darajar kudi a

cikin

raina fiye da bukatun da suke gina zuciyata ba,

idan dai zan samu in ci kuma in nema dai dai

gwargwado in samu ba zan rasa ba, wannan ya

wadatar da burina,don haka ki cire min

maganar

kudi a zamana da Alh na baya,ko hasashen na

gaba". Laila ta yi tsuru tana kallonta cikin

bugun

zuciyar fargaba yadda fatima ke son ta fifita

mijinta na yanzu a fakaice,don haka da ci da

zuci

ta ce mat. "Wannan ce hujjarki ta share guri ki

zauna a wannan kejin gidan,kuma don tsabar

zubar da aji tare da wasu mata har biyu

wadanda

ba su wuce 'yan share sharen ki ba a matsayin

kishiyoyinki?"

1 · Like · React · Report · May 17, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji 2

29) Sai yanzu ne ma zuciyar fatima ta kuntata

da lamarin Abdullahi,wanda ta tabbatar ba zai

wuce na tuna su sadiya ba, ta kyale baki ta ce.

"Ko daya,ya kankane ni ne,amma kullum ina

iyakar kokarina,yanzu ma da kika ganni asibiti

zani a yunkurina na zubar masa da ciki". Laila

ta

zaro ido gami da dauke numfashi ta dafe

kirji,ta

ce. "Ciki fatima? Da wannan kazamin yaron

kika

yarda kika sami cikin?" Ga mamakin fatima sai maganar laila ta yi mugum bata mata rai,musamman ta kiran Abdullahi kazami. Ta jima tana kallon laila sannan ta kawar da kai tana bin talabijin da kallo cikin tunanwan abdullahi da suka karade mata kwanya musamman a safiyar yau. Ta juyo ta dubi laila da bindin ido,ta ce. "Wai cewa aka yi miki gardi na aura ne?" Laila ta tare ta da cewa. "Kwarai da gaske! Ba na ji an ce wani dan malam ba ne da ya ki halin malam... Duk tsiya kuwa na san duk inda gidandanci yake a nan ya yi gida ya tare...." Fatima ta tareta da dariya. "Gaskiya to kin jahilci waye malam,ni dai zan iya ba ki shaidar malam ya fi ko wanne namiji iya soyayya,watakila don shi ya karanta ya san wace ce mace,ke nan ko kazami ne zai iya ribatata masu rikita lissafi kamar Abdullahi,idan

ban rufe ki ba fa ke nan!" "Ya kamata na ganshi".

Da kalmar da laila ta fanshe mamakinta ke nan,fatima ta ce. "Sai ki sami yammaci ki zo,ko kuma wani week end" Laila ta sauke gwairon numfashi ta ce. "Shi ke nan,mu ajiye maganarsa

gefe mu yi ta alh.bayan doguwar jinyar da ya sha

a dalilin cin amanar da kuka yi masa,jiya ya dawo da alama kuma ya kasa ganin laifinki,shi har yanzu sabuwa kike cikin zuciyarsa,ya bukaci na zo ki sanar da ni bakin zaren idan akwai hanyar da zai fara warwara bayan nasa matakin

da yake shirin dauka wai duk dan a samu wannan

kallagaggen yaron ya sahale miki...." Fatima ta yi

murmushin yake,ta ce. "Wallahi ni babu wani mataki da zan iya dauka akan Abdul laila... Ya fi

karfina,kawai sai. Dai mu taru a bangaren Alh....,sai dai ina rokonki abu daya,kar ki sanar da kowa maganar cikin nan shi kuma alh kun

hadu ki sanar masa matakin da yake shirin

dauka

in dai zai fallasar da maganar auren kinsan

wutar

da na yi,to ya canja wani dan ba karamin

hatsari

maganar nan take da shi a kunnen kawu ba....

Kuma bana son abin da kawu zai la'ance ni....

Dan bai taba wulakanta diyancina ba, na

tabbatar

idan ya tsine min sai ta bi ni". A sanyaye laila

ta

ce. "In Allah ya so haka ba zata faru ba, da

kanki

ma zaki iya sanar da Alh,zo na kai ki asibiti ba

sai mu biya gidansa ba idan mun dawo...."

Fatima ta tare cikin zare ido. "Kina da hankali

laila? Idan tsautsayi ya hado ni da abdul ya

ganni fa... Ko kuma ya dawo gidan bai tarar da

ni

ba...." Cikin rashin ko'inkula laila ta ce. "Sai ya

yi miki abin da muke so kawai..." "Tunda ba shi

kadai ne matsalaha a lanurana ba, ina son

hada

dukkan burikana a lokaci daya,sakina da kuma

rufin asirina,da kuma rabuwa da Abdul

salin'alin

ba tare da na tafi da kewarsa ba, na tabbatar

idan na rantse ba zan yi kaffara ba, Abdul ya fi

Alh sadaukar min da rayuwarsa,don shi mai

kadan ne, yake kuma sadaukar min da kadan

din

ya hada min da lokacinsa da KWANJINSA,

sannan

da asarar farin cikinsa ta hanyata batare da ya

nemi fansa ba. Amma Alh fa! Duk kofar kishin

bakuta da yake toshe min da kudi yake toshe

min, wadanda ya mallake su babu adadi,kuma

yana fanshea da abin da ya aure ni

dominsa,wato

kyau na da nunawa duniya da abokansa

kyakkyawar matar da ya aura". Laila ta rasa

abin

da zata ce mata,sai ta dau jaka tana cewa.

"Taso

mu tafi in yaso idan mun dawo asibiti sai mu

biya a sai waya wadda za ku dinga tattaunawa

da Alh,sai kuma ki san hanyar da za ki boye ba

tare da ya kamaki da kokawa ya karbe ba".

Fatima ta san magana ta fada mata, amma sai

ta

kyale ta ta buge fa murmushi kawai ta mike ta

yafa mayafi suka fice ba tare da ta yiwa su

Hindatu sallama ba.

2 · Like · React · Report · May 17, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji 2

30)

Bayan laila ta sami wurin ajiye motar,ta fito ta

rufe tana kallon yadda fatima ke waiwaye

waiwaye ta kasa fitowa cike da mamaki laila ta

ce. "Wai wa kike son gani?" Fatima ta balle

murfin motar ta fito tana cewa. "Ko dai waye

bana son gani,ina fargabar kar na ci karo da

Abdul". Laila ta yi dariya ta ce. "Ina mamakin

yadda kike shakkar wannan mutumin wanda ke

yakamata ya yi shakka musamman da yake son

zama da ke karfin hatsi....". Suka jera zuwa

cikin

asibitin fatima na cewa. "Har yau ni ma

wannan

shakkar ke damuna,mutum sai ka ce wanda ya

yi

min sihiri,gaba daya ya mayar da ni wata

kidahuma". A kufule laila ta ce. "To wa ya

sani?"

Sakon zuwan fatima na isa ga likita,kafin ya ba

ta izinin shiga sai da ya kira Abdul a waya.

"Fatinma fa ta iso". Zuciyar Abdul ta buga,ya

ji

labarin kamar wani sabo a kunnensa da

sha'aninsa da fatima A rikice ya ce. "Dr da

gaske

fatima ta ke zata zubar min da ciki?" Likita ya

yi

ajiyar zuciya ya ce. "Ya wuce wai, tunda ga ta

ta

zo...." Suka ja shiru saboda likita ya rasa abin

cewa,Abdullahi kuma yana kokawa numfashinsa

da ke son ya tsaya cak! Har sai da ya sami fitar

da kwalla,sannan ya sami bakin magana.

"Likita

ba za a iya yi mata aikin daure bakin mahaifar

a

yau ba? Tunda kwanaki suka rage ya cika

watanin hudu?" A nutse likita ya amsa. "Za a

iya". Abdullahi ya yi ajiyar zuciya ya ce.$ "to

taimakon da zaka yi min ke nan, yi mata

wannan

aikin a matsayin na zubar da ciki,ku rabu lafiya

in

ta dawo gida sai mu hadu,duk da ina son shigowa asibitin yanzu".. Da karsashi likita ya ce.

"Shi ke nan ka kawo shawara mai kyau,Allah kuma ya saukaka mana al'amuran...ya inganta abin da aka samu, ya albarkace shi".$

Abdullahi

na nade kwallarsa ya ce. "Amin na gode". Suka sauke waya,sannan likita ya kira abokin aikinsa,suka dan yi tattaunawar sirri,kana ya yiwa fatima izinin shiga. Ko gaisawa ba su yi ba ya mike yana tattara takarda ya ce mata. "Ina fatan yau ba ki ci komai ba?" Ta gyada kai cikin shan kamshi,ya ce. "Kin tabbatar?" Ta gyada kai,laila ta yi karaf ta ce. "Ai na yi zaton allura zaka yi mata". Ba tare da ya dube ta ba,ya ce. "A'a aiki za a yi mata a fitar da shi kawai".

Fatima ta zaro ido cikin dukan zuciya a tsorace ta ce, "Anya likita babu matsala? Ni da nake so ka yi min komai yanzu na koma gida,zaka kinkimo min aiki,ya ya zai zama sirri,

maigidana

yana da matsala fa Dr..." Ya yi mata wani duba na mamakin zuciya ya kawar da kai tare da

shanye mamakin,ya ce, "Kar ki ji komai za ki koma gida nan da karfe biyar ko hudu..." Ta tare.

"Lallai da sake,to ai hudu zuwa biyar din yake dawowa... Ba ni da wani uzuri da zan iya gabatar

masa na gamsar da shi". Cikin basarwa likita ya ce. "Ni kuwa da ina masa kallon wani sassaukan mutum..." Ta yi karamin tsaki ta ce. "Ganin kitse

kake wa rogo, tsabar son mulki ke sanya shi hayaniya,mutum da kafarsa sai ace sai ya nemi dama kafin ya fito.ita ma sai an ganta za a ba shi...yanzu dai me ye abin yi?. Ya kada kai ya ce.

"Babu wani canji,sai dai da yake kina tare da wannan malamar,karfe uku sai ta mayar da ke gida ki karasa wartsakewa a can. "Har yanzu fatima ba ta gamsu ba,da yanayin jimami ta ce. "Kana ganin mai gidana ba zai fahimci halin da nake ciki ko wani na kusa da ni ba?" Likita ua amsa da cewa "Ina ganin ba wannan me mafi a'ala tare da ke ba, kin sani cikin da ya kai watanin hudu aka cire shi dole yanayinki ya canja,sai dai kawai ki san hikimar da zaki yi

wajen sanar da mai gidanki zubewa cikin,ko bai san da shi ba?" Sai ta gyada kai. Laila kanta sai da ta ware ido tana kallon fatima, kafin ta girgiza kai ta ce. "Sai dai kawai ki ce kun nunke juna kawai cikin fa ya turo sosai, sai idonsa ya kasa gani? Ke dai kawai ki zubar komai ta fanjama fanjam!" Da haka suka rufe tattaunawar aka fara shirye shirye shiga da ita dakin tiyata31) Abdullahi na tsaye kan fatima a dakin da aka turo ta bayan kammala tiyata fana baccin nan mai kama da mutuwa. Ya kurawa fuskarta ido sai zubar da hawaye yake na ciwon ran yadda fatima ta dage da sai ta salwantar da musu dan da suka yi shekaru sun tsumayi daga shi har ita,wannan wanne irin son zuciya ne? Anya kuwa a duniya akwai fitiniyar mace irin fatima? Tun yana karfin halin dauke hawayen nasa har ya hakura ya bar shi yana ta zuba. A haka likita ya kama shigowa ya same shi,ya ce masa. "Hakuri zakayi Abdullahi,insha'Allah komai zai zo da sauki baby ciki koshin lafiya cikin mu kuma ya yi nasara.

Abdullahi ya nacewa kallon fuskar fatima

sannan

ya dubi likita yana goge hawaye,ya ce. "Mata

lamarinsu na da wahalar da numfashi. Wallahi!

Musammam kuma irin su fatima,na rasa abin da

yarinyar nan ta ke shiryawa rayuwarta,kina

gidan

mijin ki ki dinga gudun haihuwa,alhalin ba ki da

damar yankar wani tikitin sabuwar wata

rayuwar.ga wadda ke hannunki kuma shekaru

na

shurawa,ko don ta ga ku da zabi kyawunta zai

hana ku ganin munin aikinta in ma kun gani

kun

rabu da ita akwai masu rububinta? Abdullahi bai

musa ba,sai dai ya yi tawili. "Haka ne! Kuma da

taimakom son wanda ke hana ganin aibu. Amma

duk wadannan dalilin biyu ba su hana ni dora da

KWANJI a cikin tarbiyyarta ba, nake kuma

hadawa da addu'a don haka nake ji a

raina,zan

iya toshe duk wata kafar da zata fandare

hanya,wanda ya fi karfinma kuma na san

ubangijina zai min". A sanyaye Dr ya ce. "Na ga

wannan alamar". Yana tuno kalamanta na

dazu.

"...maigidana yana da matsala fa Dr". "..... Ba

ni

da wani uzuri da zan gabatar masa na gamsar

da

shi. "..... Tsabar son mulki ke sanya shi

hayaniya". DuKkan wadannan maganganun

nata

suna bayyana shakkarsa ne,wanda da ba ta yi

ba

karamin cin kashi zata yi akan sa ba. Likita ya yi

ajiyar zuciya,ya ce. "Yakamata ka tafi dan ta

kusa farkowa,me rakota ma na tabbatar ta kusa

dawowa". Abdullahi ya kara zubawa fatina ido,

sannan ya dubi Dr ya ce. "Dr idan ta farko ka

ga

tana cikin wani hali kar ka sallame ta, ka yi

mata

dabara ka ce zaka sanar da ni ta dabara,ya da

za

a barta cikin wani hali ba," Dr ya dafa

kafadarsa

yana cewa. "Kar ka ji komai,in dai hakan ta

faru

wanda ba a fata zaka ji wayata". Suka yi

sallama

ya fice. Bai iya komawa wajen aikinsa ba sai

kawai ya wuce gida cikin bacin rai da tashin

hankali.ya tsaya masallaci ya sallaci la'asar

sannan ya shiga gida. Jin shigowarsa ya sa

sadiya ta ji kamar ta zuba ruwa kasa ta sha

saboda murna. Ta dinga tsaiwa jikin taga don ta

hango shi yana rankwashin dakin fatima,sai ta

ji

shiru ya bata a dakinsa. Ba ita yakamata ta je

dakinsa ba don Hindatu ce mai karbar

girki,amma

kawai sai ta yi shahada ta mike ta tafi dakinsa.

Ta same shi zaune yana karatu kur'ani fuskarsa

a

jagule,don ko kallonta bai yi ba, ya fake da

karatun da yake. Don tsabar tsuguddi abin da ta

jima ba ta yi masa ba sai ga ta tana yi

masa,wato ta tsuguna gabansa ta zare masa

safar kafa,ta kunce masa neck tie ta zare masa

coat sannan ta wuce da su dakinsa ta fito ta

kawo masa lemo da ruwa.ta nemi guri ta zauna

tana jiran ya diga aya.ya gama haka ya ki

tsayawa ya tanka ta,sai da ta zauna sosai sai

murmushi ta ke masa, shi kuma ya yi fuska. Ya

rufe kur'ani yatsunsa na inda yake ya dube ta

yana kokarin hadiye bacin ransa,ya ce. "Kun

wuni

lafiya?" Ta muskuta ,ta ce. "Lafiya kalau.ko

dai

ka ce na wuni lafiya. Tunda Hindatu ba ta nan,

fatima ma haka". Ya yi saurin duban agogo

fuskarsa a bace. "Au Hindatu ba ta shigo ba?

Kamar ban ce kar a dinga fice karfe hudu a

waje

ba?" Ta tari numfashinsa da cewa. "To ai ita ma

fatima ba ta dawo ba" Cikin rashin kulawa ya

dauki wayarsa ya fara dubawa,ya ce. "Mun yi

zan

je na dauko ta,ban sami dama ba amma na yi

waya a kawo ta yanzu. Takaici ya lullube

sadiya,ta zura masa ido da duban tuhuma.

"Tunda idan na je unguwa kana zuwa ka dauko

ni

ko ka dauko Hindatu ko?" Shi ma ya zura mata

ido. Ba tare da fuskarsa ta karbi korafinta

ba,ya

mokade lebe ya ce. "Ko a gadon baya na zanm

daukota bai kamata ranki ya sosa ba,matar da

ta

ke da motocin hawanta na hana ta kawo su

gidan nan ke kin ga yakamata na barta tana

yawan motar haya? Wani lokacin idan kika tashi

korafinki sadiya ba kya hada shi da hankali

wallahi... To kin ga ba na son hayaniya,ki tashi ki

koma dakinki kar ita ma waccan ta shigo ya

zama wani korafin na daban ku da kullum abin

neman masifa ba ya yi muku kankanta. Kafin

ma

ta sami bakin magana ya tashi da alkur'anisa ya

shige daki,n ta fice dakinta.

2 · Like · React · Report · May 17, 2015

Ummee Amina

hmm

Like · React · Report · May 17, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji 2

32"Dr

wannan wanne irin Abortion ne na ga cikin nata

kurcici?" Tamabayr da laila ta yiwa Dr ke nan

lokacin da ake ta faman cike takardun daukan

fatima zuwa gida,wadda ke kwance tana mayar

da numfashin. Dai dai. Dr ya ki nuna damuwa

da

korafin na laila.,ya ce. "Zai sace nan da

kwanaki

bakwai,illa dai a kiyaye dokokin nan kar ta yi

aiki

mai wahala, ban da shara,ban da daukar ruwan

wanka.ke ban da komai ma sai dai ta ci ta

kwanta,abincin ma kar ta ci me nauyi...kin

gane?"

Ta gyada kai idon ta na kan fatima wanda ke

tambayarta lokaci da hannu,laila ta yi tsaki ta

ce.

"Wai dafa ki zai yi ne kika damu haka? Wannan

ma tsabar zubar da aji ne ki dinga tsoron namiji

haka". Dr ya dinga nazarin laila a fakaice

sannan

ya ce mata. "Malam laila ke nan,ashe zubar da

aji ne don mace ta yi shakkar abin da ran

mijinta

zai sosu.... Ko kin manta abin da ta yi laifi ne

babba?" Ba tare da laila ta dube shi ba, ta ce.

"Mazan ma suna suka tara,in ni ce da wannan

mijin na rantse ki zagina ya yi sai na rama"

Murya a shake fatina ta daga mata hannu,ta

ce.

"Ba na son cin fuska laila". Dr ya dube ta ya

dubi

fatinma,ya ce. "Anya kuwa kin san abdullahi

da

kyau?" Laila ta yi tsaki kawai ta kawar da kai

tana son maganar ta bi ruwa,shi kuma dr ya

nace

a yi ta, ya ce. "Laila kin fin kanwar nan taki

zafin

kai" Ta amsa masa da cewa$ "Ba kanwata ba

ce,kawata ce". Dama abin da yake son sani ke

nan,don kai wa Abdullahi tahoto,wanda ya

tabbatar laila ce ke zuga matarsa. Da haka ya

sallame su da taimakon nurse suka kai fatima

ba

cikin hayyacin ta ke sosai ba,dukkan

sambatunta

na fargabar kar su tara da abdullahi a gida ne,

tare da rokonm Allah kar ya sa ma kar ya san ta

fita. Sai dai kash! Sai ga ta a zaune bayan sun

shiga harabar gidan ta ga motarsa,numfash inta

sama sama ta dafe kirji ta ce. "Na shiga uku

laila,ya dawo wallahi". Laila ta zuba mata iso

cike da takaici. "Kin fara kai ni bangi

wallahi,wai

rufe ki da duka zai yi ne? Iyakacin ya ce ki

koma

nida kika fito,ba shi kenan ba,dawa ta yi

nama...." Fatma ta tareta da cewa. "Zai iya

dukan nawa,ko ma abin da ya fi dukan,in koma

inda na fito din ne kuma na tabbatar ba zai

fada

ba". A kufule laila ta ce. Wannan fargabar ta

kori

jirin da ke damunta,bakin fal addu'ar su shige

suruf ba tare da sun ci karo da abdullahi ba.ta

taka da kafarta suka shiga cikin gidan.

Abdullahi

na tsaye ta taga yana kallonsu har suka bude

dakin fatima suka shiga.ya saki labule ya tafi

gadi da sauri ya zauna lokaci da ya ji shi ma jiri

na kwasarsa,ya ma rasa irin matakin da zai

dauka akan fatima bare laila. Fiye da mintuna

goma yana zuba idon ganin fitowar laila,sai da

ya

ji buruntu kicin din fatima ya san kila ghirki ta

ke

mata. Zuwa wannan lokacin zuciyarsa ta rage

tafasa,ya shawarci kansa yin hukunci a

nutse,ba

da fushi ko gaggawa ba. Har yanzu hankali

fatima bai gama kwanciya ba, tana sha tea a

hankali idonta a kofa, kunnenta a kan juyo

motsin

bude tasa kofar.can ta ji sallamar

Hindatu.lokacin

daya da bude kofar dakin nasa ya fara juyewa

hindati nata sababin da kakkausar murya.

"Duba

agogon hannunki karfe nawa?" A ladabce ta

fara

in ina. "Ka yi hakuri... Wal wallahi go slwo ne ya

rike ni.amma tun uku da kadan na fito". A

zafafe

ya ce mata. "Da ya rike ki ai sai ki kwace ki koma

inmda kika fito tunda na ce in dai an san za a

wuce karfe hudu a waje gara a tambaye kwana.

Ta kuma kwaso wata magiyar. "Don Allah ka yi

hakuri Abu Turab.." Ya kuma tarewa da bala'I.

"Kin ga Hindatu kar ki kara fado min wata

magana, da hakuri da rashin jin maganar tawa

duk ki ci gaba da tanadar min su ai dan inyi ta

fama da su na zo duniyar". Ta yi shiru kanta a

kasa,ya kuma sauke huci,ya ce. "To ki sha

kuruminki idan ma kin yi haka ne don ki bata

min

rai, to tare da naki kika hada wallahi na da

wata

daya da wasa kar inji kin tambaye ni fita".

Gaban

fatina ya ci gaba da dukan uku uku ta yi kasake

da tea a hannu,laila kanta sai da ta ji abin a

jikinta,ta ce. "Fatima,wannan wane irin dan

sababi ne?" Hankali fatima kamar ba ya tare

da

ita ta ce. "Laila rufo mana kofar nan kar ni ma

ya

zo ya sauke min nawa wanda na tabbatar sai ya

fi nata tsauri". "Insha'Allah ba zai shigo ba".

Sai

ga shi kuwa addu'arta ta karbu,don ficewa ya yi

daga gidan sai tashin motarsa suka ji. Fatima ta

sauke ajiyar zuciya kila wa kalanci,wato ko dai

Abdullahi bai san ta fita ba,ko kuma cikin nata

hukuncin ke nan. Laila ta yi ta kwantar mata da

hankali,sannan suka yi sallama da zummar gobe

zata dawo ta dubata kuma zata taho mata da

waya.

2 · Like · React · Report · May 17, 2015

Amierah S-Man

ndalin hausa novels

Zuciya d kwanji 2

Sai da bacci ya fara fizgarta a nan falo ta ji

bugun kofa. Ta dubi agogo da sauri cikin bugun

zuciya, agogon ya nuna tara da rabi,ta yi baccin

rabin awa ke nan,domin ta ga tsinken agogon

akan tara dai dai saboda kasa kunneb shigowar

abdullahi bai shigo ba, har baccin ya dauke ta. A

tsorace ta ke, don haka ba ta bude masa ta dawo

falon ta zauna tana jiran tasa karsasowar. Bai

ko

dubi inda ta ke ba, fuskar nan tasa a murtuke!

Ya

dinga shiga da kayan masarufi store dinta, har

ya

gama ya dawo falon ya kwashe kayan tea din da

ta shi da gwangwanayen lemon da suka sha ita

da laila,ya wuce da su kicin. Sannan ya dawo ba

tare da ya dubeta ba ya ce "Me za ki ci?" Ta

dube shi da kyau,sai ta ji shakkarsa ta kara

rufe

ta, tana in 'ina ta ce. "Na ..... Na sha tes ya

gamsar da ni" Ya mokade lbe, idonsa akan

talabijin ya ce. "Kin yi wanka?" Girgiza kai

kawai

ta yi, amma da tasan ba lallai ya san ta yi ba,

tunda ba kallonta yake ba, a hankali sai ta ce.

"A'a Kawai sai ya wuce dakin baccinta zuwa

bandakin ciki, ya tanadar mata ruwan wanka

mai

saukin dumi,sannan ya kirata daga cikin dakin

ya

yi kiranta da murya babu walwala. "Ki shigo ki yi

wankan". Ya kamata ace ta taya shi wannan

danyan kan nasa, amma ita ma sai ta ji a

ranta

gara ta lallaba shi tunda ta riga ta yi

laifin,laifin

da ya sha fada mata hukuncinsa zai iya zama

ba

fallasa sirrinta ga kawu,wadda ta ke jin gara

mutuwa akan haka. Ta mike da kyar ta shiga

dakin a hankali saboda ciwon da dukkan

gabobinta suke babu ma abin da ya fi damunta

irin yadda cikinta ya dameta da watsal

watsal,sai

ka ce akwai dan da ke mata busharara shi ba a

cire shi ba. Ta same shi gaban dressing table

yana feshe kayan baccinta da turare,daga nan

ua

fara ware mata bargon kan gadon yana rage

fulullaka yadda dai zata sami komai cikin sauki,

wannan kyautatawar tasa ce ata sa ta rashin

ganin aibun fushinsa,har tausayin sa ya sata

jin

kwalla ta taru a idanunta. Yadda ta ke jan

numfashi ya sa dole ya dan dora mata ido a

fakaice,ita ma tana satar kallonsa ta yi saurin

daure numfashin ta shige bandakin ko kayan

jikinta ba ta rage ba. Har man wanke baki ta yi

wankan ta gama cikin hawaye don haka har ta

same shi zaune kan stool cikin zurfin

tunani,cikin

dar dar ta wuce ta dauki kayan baccin,ta juya

baya ta saka ba tare da ta nemi ko shafa mai

ba,

ta haye gado ta ja bargo ta lumshe ido. Kamar

daga sama ya jefo mata tambaya muryarsa a

cushe. "Zan iya sanin inda kika je yau?" Ta ji

numfashinta na neman sarkewa saboda fargaba

da neman amsar da zata ba shi don haka suka

kwashi lokaci yana jiran amsarta har ya kuma

cewa. "Wai ba ki ji ba ne?" Rukani ya sa ta tashi

zaune ba tare da ta shirya ba, tana dubansa kai

tsaye ta ce. "Ni babu inda na je". Ya kara tara

gira yana dubanta,ya ce. "Ko? Amma na dawo

ban tarar da ke ba,kuma ina cikin gidan nan

kika

shigo. Ta kawar da kai daga gare shi,ta ce.

"Gaskiya ba in ba ce, don ko kofar daki ban je

ba". Ya sauke nufashin yana girmama karfin

halinta,ya kawar da kai cikin cije lebe,ya ja

fasali

sosai sannan ya kike tsaye ya dubi tsabar idonta

ya ce. "Fatima kai ki mayar da ni dan iska kin

ji!

Kar kuma ki taba tsammanin sonki ya yi min

runtsewar idon da zaki ci kashi a kaina na zuba

miki ido... Na ce dole ya zama da izinina, kuma

dole hakan ce zata kasance wallahi ban fada da

zummar waka ba! Shugabancina a kanki da

matsayin aurenmu kamar sauran aure a

musulumci ba zai taba canja salo da ka'idoji ba

wai do ba kya sona ko ba kya son ki zauna da ni

ni da nake shugaban da KWANJINA nake motsi.

Kamar yadda ba ki da ikon sakin kanki haka

zalika ba ki da ikom canja matsayin biyayyarki

gare ni zuwa yin komai na radin kanki.... Na

rantse miki ba ki isa ba wallahi.... Kin yi na farko

kinyi na biyu, kuma kin yi na karshe,duk ranar

da

kika kuma saka kafa kika bar gidan nan sai na
yi
miki rashin mutumcin da har ki mutu ba zaki
manta da ni ba. Kin fara fitina ta
wallahi,hakurina
ya fara taba bango a lamarinki... Na fada miki
na
kuma har abada babu saki tsakanina da ke,
hakan kuma ba zai sa na laminci abin da raina
ba
ya so a cikin lamarinki ba. Idan ma kin sami
dan
iske ki sanar wa Alh da kike zuwa wajensa...
Kuma idan kun ci amana ta Allah ya saka
min...."
Bai saurare ta ba sai ya fice ya bar ta baki bude
kekkece saboda kuna. Ta yi kuka, ta yi kuka ba
ta da me rarashinta,har sai da zazzabi ya rufe
ta
sannan ta koma ta tasa inda kudundunar tana
faman makyarkata.ina ma daga haka ta
zarce,ta
huta da wahalar wannan rayuwar da mutum na
ya samun abin da yake so. Haka ta kwana tana
makyarkyata,ga dukkan jikinta yana

ciwo,mararta

ma ta kulle tana ciwo, sai ta rasa inda zata

tsoma ranta,Allah Allah ta ke gari ya waye ta

nemi dauki,don haka da ta yi sallah asuba ta

dinga kasa kunnen shigowar Abdullahi har zuwa

lokacin da zai shigo mata.... Amma bai shigo

gidan ba sai da rana ta fito bakwai da

rabi,wanda

wannan lokacin ma ya gama shirin fita ofis.

Yana

shiga dakinsa Hindatu ta cimmasa ta durkusa

har

kasa ta gaishe sji,sannan ta mike a ladabce ta

ce, "Abu Turab wai duk fusjin ne? Don Allah ka

yi

hakuri". Ya girgiza kai da sauri da son ya yi

murmushi,ya ce. "Ya wuce wallahi" Ta ce,"ban

ga

alamar hakan ba,jiya fa baka yi baccin kirki ba,

ka fice sallar asuba ba ka shigo gidan ba sai

yanzu. Ina ganinka ka shigo babu walwala,sai na

ga me ya yi zafi?" Ya share fuska yana kawar

da

kai,ya ce. "Ba wannan matsalar ba ce,akwai

abin

da ke damuna... Ku saka ni cikin addu'a". Cikin tausayawa ta ce. "To Allah ya warware". Ya ce,"amin, yi min afuwa na ga fatima ba ta da lafiya" Ta yi saurin gyada kai tunda tana son ya huce,ta ce. "Babu komai". Ya yi mata godiya ya juya ya fita. Ya same ta kudundune a gado tana ta faman kuka da makyarkyata,ya kara daure fuska don ya yi tsammanin kukan rikicin da ya yi mata jiya ta ke, don haka ya yi mata banza ya fara abin da ya kai shi, wato gyaran dakin, amma makyarkayartar da ta ke ya sanya dole ya sanya mata ido,murya a cushe ya ce. "Wai wannan kukan na jin dadi ne ko na me? Ni ya kamata na koka don ni kika cutar,me yasa kike son nuna ke aka cuta?" Ta girgiza kai cikin wahalalliyar murya,ta ce. "Abdul ba ni da lafiya,zan mutu wallahi! Da sauri ya yar da sallayar da ke hannunsa ya isa gabanta,ya ture bargon ya dago

ta a rikice ya ce. "Me yake damunki?" Ta cije

lebe

cikin sartun hawaye tare da rike hannunsa da

kyau ta ce. "Cikina Abdul zazzabi kaina.." Ya yi

saurin tattarota jikinsa yana rungumewa,cikin

nuna damuwa ya ce. "Ciki kuma fatima...

Wanne

irin ciwon ciki? Sannu.... Ko mu je asibiti?" Da

sauri ta girgiza kai tana kara jankane shi. "Ka

yi

min addu'a kawai... Idan ya yi min sauki ina da

magani zan sha..." Ya ce,"to... To shi ke nan....

Dai dai ina ke miki ciwo a cikin?" A rude ta ce

masa "Ko ina abdul" Ya dagota ya yaye cikin

yana kallo,hankalinsa ya rabu biyu da addu'ar

da

kuma kallon yadda cikin nata ke ta faman

motsi

alamar dai an kuntata shi. Suka kwashe lokaci

mai tsawo a haka,cikin ikon Allah sai ga sauki ya

samu har ta yi bacci a cinyarsa. Ya kara damke

hannunta cikin nasa yana bin fuskarta da

kallo,kwalla ta fara cika masa ido, lokaci daya

ta

rame kamar wadda ta shekara a kwance. A haka

ya share mintuna ashirin ko kwakkwaran motsi

ba ya so ya yi don kar ya katse mata bacci,har

sai da Hindatu ta fado masa a rai, sannan ya

lalubo wayarsa a hankali ya kirata. "Ki yi hakuri

Hindatu,mun ciki wata matsala ne,kar ki ji ni

shiru". Duk da zuciyarta a jagule ta ke,sai ta

daure ta ce. "Babu komai,ina fatan ba jikin ba

ne?" Ya ce,"shi ne wallahi". Cikin bayyana

damuwa ta ce. "Ayya! Allah ya kawo sauki,ko ni

zo akwai abin da zan iya taimakawa? Da sauri

ya

ce da ita. "Yauwa da na gode miki kuwa". Ta

sauke waya da sauri ta zura takalmi ta nufi

dakin

fatima. Ita kanta hindatu kallo daya ta yiwa

fatima ta san lallai tana jin jiki,cikin bayyana

damuwa ta ce.

3 · Like · React · Report · May 17, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

34

"Subhanallahi,me yake damunta haka?" Ya

dan

muskuta a hankali yana gyara mata kwanciyar

don ya ji dadin zama,ya ce. "Daga zazzabi ya

koma ciwon ciki,da kin ganta a dazu sai kin
mata
hawaye..." Hindatu ta ce masa. "Gaskiya dubi
yadda lokaci daya ta rame, wannan ai sai ku
tafi
asibiti,da me zan taimaka maka? Ya ce,"da
ruwan
zafi a fulas,wanda zata sha tea sai ki dan gyara
mata kicin ki wanke mata kwanuka.idan har kin
gama ba ta farka ba,sai ki zo ki dan hada mata
ruwan wanka sai na tashe ta". Hindatu har
zuciyarta ta ce. "To,babu laifi". Da sauri kuma
ta
fice kicin din tan aikin da aka sa ta, har ta
gama
ta je ta hada mata ruwan wanka, sannan ta
sanar masa tare da cewa. "Yanzu haka ba ta yi
baccin dare ba shi yasa yanzu ta ke fanshewa".
Ya ce,"ni ma na yi tunanin haka". Ta
ce,"yanzu
haka zaka tashe ta? Ya amsa mata da cewa. "Ai
ya zama dole, gara ta tashi ta sha magani". Ya
sunkuya ya fara hura mata kunne,ta motsa a
hankali tare da salati tana dafe ciki,ya dago ta
a

hankali suna yi mata sannu shi da

hindatu,muryar

hindatu ta sa ta bude ido da sauri tana binta

da

kallo,ta sauke ido akansa da tambayoyi a ido iri

iri,da ya kasa amsa mata sai ta ja jiki a hankali

ta janyo filo ta kwanta.ya suke kafafunsa yana

cewa. "Ki tashi ki yi wanka,ki samu ki karya ki

sha magani". Ta girgiza kai a sanyaye ta ce.

"Ba

zan iya ba..."$ "sai na taya ki". Ta tari

numfashinta da fatar hakan,amma sai ta yi

mursisi ta kara jan bargo tana cewa. "Abdul bar

wankan nan don Allah". Cikin tausayawa ya ce.

"An bar shi, sai ki wanke baki ki dan kurba tea

don ki samu ki sha magani". Ba ta tsinka ba, ya

tashi ya kawo mata tasa da brush ya taimake ta

ta tashi,hindatu ta dago tasan ta zuba mata

ruwa

a brush din ta mika mata, tana mata sannu shi

kuma ya tsaya hada mata tes din. Da kansa ya

dinga ba ta da cokali tana sha tana faman rike

ciki,saboda karta da yake mata har ma shan ya

gagare ta, dole ta koma ta kwanta tana juyi.

Babu shiri Abdullahi ya fice waje ya kira likita a

wayarsa cikin tashin hankali ya ce. "Dr akwai matsala fa, ciwon ciki ya matsa mata matuka... Yakamata ka zo ka taimaka ko kuma mu zo." Dr ya tausaya,sannan ya ce. "Hakan zata iya faruwa,a cikin magungunan da na ba ta har da na

wannan matsalar me yiwuwa ba ta yi amfani da su ba ne, ka bincike su,amma idan ya ki tsayawa nan da yamma sai ku zo". Ya yiwa dr godiya sannan ya koma dakin da sauri. Ya ce mata. "Ina

magungunan?" Da kyar ta amsa masa. "Suna falo" Ya fita da sauri,hindatu kuma ta bude karamin firij din da ke kusa da ita ta dauko ruwa,tun ma kafin ya karsaso ta zuba a tambulan

tana jiransa,suka bata ta sha ta yi mata sannu,can ciwo ya dawo sabo,hankalinsu gaba daya sai da ya tashi. Haka suka yi ta fama,abdullahi na faman yi mata add'a a cikin,hindatu ma na tata a cikin zuma har Allah ya kawo sauki bacci mai nauyi ya dauke ta. Wunin ranar nan kusan a haka ta yi,don haka ko

aiki abdullahi bai leka ba, hasalima masallaci

kawai kan fitar da shi. Hindatu kuma tsurku

biyu

ya hade mata,ga na tabatar kallon fatima da

ciki,ga na lissafin kwatancin matowar da

Abdullahi ya yi akan fatima wadda sam ba ta

damu da shi ba.tunda hindatu ta ke da

Abdullahi

ba ta taba ganin hawayensa ba, amma a yau

inda

tana da bukatar tarar hawayen ko gwanhwanin

madara ne sai ta samu, wannan abu yana

matukar daure mata kai, sai dai wannan bai

hana

ta hadiye kishinta ba,suka dinga hidimar

fatima

tare har dare,bayan iska lokacin da ciwon ya

jima

bai motsa ba. Wannan kokarin nata da

kyautatawar ne ya sanya Abdullahi jarumtar

barin

fatima hannun Allah,lokacin da dare ya yi, don

dai

kar ya cika shiga hakkin ita Hindatu,ya yiwa

fatima bankwana tare da bar mata daya

wayarsa

da zummar ko wani abu zai faru sai ta kira shi.

Yana dab da ficewa daga dakin ya ce mata.

Biyewa shaidan idan ya zuga ki kiran Alh da

wayar don wannan laifin yana daga cikin wanda

ba zan iya yafe miki ba,zan ma dinga kaiwa

ubangiji na kararki". Ta dago cikin matukar

kasalar jiki da ta zuciya tana ture wayar

gefe,ciki

murya mara dadi ta ce. "Zo ka dauki wayarka".

Ya bata rai, ya ce. "Ai ba don halinki na baki ba,

in don halinki ne ma fadima kallonki na yi? Ko

da

yake ban sani ba ko a haduwar da kuka yi jiya

ya

ba ki wata wayar". Kai tsaye ya fice ba tare da

ya

jira cewarta ba sai ya barta da kwalla da son

fadawa cikin tunanin barkatai,mafi ciwo a

wajena,

shi ne uzurin da ya yi zuwa ga hindatu alhalin

tana bukatar kulawa.ga shi ma'abocin iya jinya

wanda ba ta taba riskar irinsa a rayuwar ta ba,

sai ta ke ji a ranta kamar idan yana tare da ita

ciwon zai fi saukaka mata.ta rasa daga inda

wannan kishi nata ke bullowa. Yana shiga ya

sami hindatu ta fito wanka da walwalarta,ta

tambaye shi. "Ta yi bacci?" Ya girgiza kai, ya

ce.

Har yanzu idonta biyu". Ta ce,"ina fatan ciwon

bai kuma tashi ba? Ya amsa,"haka ne". Ta dan

ja

fasali kafin ta dora wata tambayar, zuciyarya

cike

da fargaba. "Abu Turaba anya ba ciki ne da

fatima ba?" Dabararsa ta fara kokawar tsaida

lugunden kirjinsa, ya yi matukar juriya kafin

ya yi

fuska ya amsa. "Wallahi ba ta taba yi min

wannan maganar ba, me yasa kika fadi haka?

Cike da mamaki ta kada kai. "Ba hasashe nake

na Abu Turab,ina shakkar in fatima ba ta da

ciki

wata kila salon alakar da ke tsakaninku ne ya

hanata sanar maka kunna na yi mamakin da kai

ba ka ganshi da idonka ba,ga shi nan ya fito?"

Ta

kwaso masa rantsuwa,yana dariya ya dakatar

da

ita. "Ki daina saurin rantsuwa,gara ki bari a

tabbatar don haka ina barar sirri,ki kulle

bakinki a

kan wannan maganar,kar ki sake na ji ta a

bakin

wani". Ta dan yi kasake,sannan ta ce. "Kana

daukaka dai wata magulmaciya ko?" Ya yi

saurin

girgaza kai yana dubanta kai tsaye ya ce. "A'a

na

san ki dai da dan banzan surutu, kin san kuma

an

ce shi zance ado ne, amma kawaici kubuta ne"

Sai da ta ja fasali sannan ta dube shi da

kyau,ta

ce, "Wannan kasheda kasheda suke tabbatar

min

fatima na da ciki,kuma kasan da shi ko in ce

kun

san da shi, ban san don me kake son ka boye

min

ba. Ya jima yana kallonta kafin ya sami abin ce

mata. "In rantse miki ba mu taba maganar cikin

da fatima ba ki kasa gaskata ni? Ni ma ban san

me yasa kike son ki fitine ni akan wannan

maganar ba". Ta dinga girgiza kai fuskarya na

canjawa,muryarta a sarke ta ce. "Ba laifi ba ne

don na nemi in san cewa dama in da sadiya ne

ba ma haihuwa ke nan? Ya dinga dubanta cike

da

mamaki,sannan cikin tara gira ya ce. "Kin saka

wannan hasashen naki a magwajin hankali da

ilimi kuwa? Ina tantamar haka ban sani ba ko

idonki ne ya rufe. To amma ba zan hana ki

hasasshenki akan batun don jin wannan

maganar

a wajen ko cikin gidan ta bakinki na tabbatar

miki,ita zata sa na warware amincin da ke

tsakanina da ke. Sai kawai ta zura masa ido.bai

jira cewarta ba, ya kada kai ya wuce bandaki ya

barta da hidimar binsa da kalloZuciya d kwanji

35

*****************************

*********** Kafin ya

fita sallar asuba,sai da ya shiga dakin fatima

don

tabbatar da lafiyarta.sai ya same ta tana bacci

mai nun koshi lafiya,ya jima yana kallonta

sannan

ya farkar da ita. "Ya ya jikin?" Ya tambaye ta

bayan ta farka,ta sa masa ido kawai, mamaki

da

shakkarsa ta ke, ya bude KWANJI da kyau yana

kulawa da ita, amma fuskarta ba ta fasa nuna

yana fushi da ita ko da yake zargin da yake

mata

adalcinsa ne ma kawai ke sa shi kular da ita.wai

wajen Alh ta je, ita da kanta tana ganin abin

tir a

zargin duk kuwa da wani bangaren zuciyarta na

ganin tsabar iya mulkinsa ke son nuna mata fin

karfi wajen rabata da Alh,ba tare da yana da

wannan damar ba. Cikin sanyin muryar wanda

ya

ji jiki a cuta ta ce. "Alhamdulillah". Ya ci gaba

da

binta da kallo,fuskarsa babu walwala. "Ciwon

cikin ya kuma tashi?" Ta girgiza kai kawai.ya

kara dubanta a kaikaice cikin tare gira,ya ce.

"Amma ina ganin har yanzu akwai matsala

daga

shi nan a kumbure". Cikin dar dar ta kara jan

bargo tana rufe jikinta,sannan ta juya masa

baya,

shi ma ya fara ja da baya yana hadiye

dariyarsa,ya ce. "A'a ki tashi ki yi sallah,in dai

bai

sace ba nan da gobe dole mu je asibiti,ban san abin da ya baki kika ci ba yake neman kashe min ke,an gama da ciwo ga kumburi,kuma a haka kike

masa kallon masoyi..." Ko motsi ba ta yi ba bare alamar zata tanka, don ta dan fahimce shi,idan

yana cikin fushi ba ya son yana magana ana mayarwa.tana jinsa har ya gama zungure zungure rigimarsa ya fice. Bai kara waiwayarta ba, sai tara saura ya shigo mata da take away,ya

fara da hada mata ruwan wanka,babu walwala tare da shi ya yi mata umarnin ta je ta yi, kafin

ta fito ya gyara dakunan tsab ya baza musu kamshi. Ta fito ta same shi yana dube sube a wayar da ya bar mata,fuskar nan tasa a murtuke!

Ta dinga satar kallonsa har ta kai ga tankawa cikin dar dar din kirji. "Ko tabawa ban yi ba". Bai

ko juyo ya dube ta ba bare ya tanka,ya zura abarsa a aljuhu kawai,sannan ya janyo mata stool ya ajiye gaban mirrow har da bude mata

mayukan da ya fahimci ta fi mu'amula da

su,sannan ya koma gado ya zauna ya jingina da

allonsa sai ta share mirrow din ta nufi can

karshen gadon ta zauna ta juya masa baya.ya

dan bita da kallo.amma sai ya ki tankawa ya

tashi ya kwashi mayukan da karamin kurar

kayan

kwalliyarta ya ja ya kai gabanta har da kai

mata

foot stool,sannan ya koma mazauninsa ya kuma

zama. Ya dinga komai cikin kasala saboda ciwon

jiki da damuwa a rai,idanunsa a kanta tunda

ba

ta kallonsa,tausayinta na damursa a rai, yana

jin

ba don yana son nuna mata kurenta ba man ma

sai kawai ya shafa mata. Yana ta duban agogo

saboda lokacinsa da ke tafiya,amma haka ya

hakura ya share ta har ta gama lakakinta.ya

fito

mata da kayan sawa sannan ya mayar da kayan

kwalliyar,ta shirya ta kon sofa ta kishingida, ya

fita ya kawo mata abincin,ya zauna kusa da ita

da magungunanta a gabansa da ruwa da

tambulan a hannunsa. Ta fara karyawa cikin

kwalla,gaba daya rayuwar ta yi mata zafi,ta
rasa
gane wannan masifa in dai Abdullahi na mata
fushi sai ta rasa inda zata soma ranta gaba
daya
sai ta ji kuncin duniyar nan ya ishe ta. Abin
takaici ma abin da yake zarginta da shi ba ta
aikata ba, kuma abin da ta aikata din ba ta yi
nasara ba don ta hakkake likita yaudararta
kawai
ya yi bai zubar da cikin nan ba. To ina mafita ke
nan? Sai ta zabi farawa da maganin wannan
fushin nasa da ke kuntata mata Zuciya ba tare
da
yakamata ya kuntata mata din ba. Bayan ya ba
ta magungunan ta sha tana mika masa
tambulan
din bakinta na rawa,ta ce. "Abdul wallahi
shekaran jiya ba wajen Alh na je ba. Ya kwashi
sakkani masu dama kafin ya tanka a takaice.
"Ina
kika je? Ta dan yi wura wura tana neman inda
zata ce kamar ta ce kasuwa sai ta tuna
kishinsa,ta ce, gidansu ya kira ya tambaye su.
Kawu sai ta sami kanta da kada kai kawai ta ce.

"Asibiti na je". Ya bita da kallo,ya ce. "Kika yi me?" Sai ta ji tamabayar kamar ta gayya ko ta sanin abin da ta je yi asibiti,don haka ta kasa amsawa. Ya kara dubanta da kyau,ya ce. "Idan ba ki ba ni amsa ba zan dauka akwai wata 'yar burum burum da kike min, in baki sani ba ki sani ina zargin akwai dana ko'ya ta a cikinki, in dai asibiti kika je to ina zargin kin sonm salwantar min da ciki,wanda shi ne abu na karshe da zaki yi

min ki cuce ni,shi ne kuma zai iya sa ni jarumtar

runtse ido na yi miki rashin mutuncin da zan yi shakkar yiwa wanda na fi ki a filin duniyar nan, a

matsayinki na wadda na fi kauna a cikinta. Sai dai kar ki yi zaton rashin mutummcin shi ne saki,

har in mutu ba zan sake ki ba, sai dai ke ma ba zaki ji dadin zama da ni ba Fatima. Ta runtse ido

sannan ta bude su da ballowar hawaye.tana cikin

tsaka mai wuya ke nan, in cikin ya zube ko bai zube ba, duk babu sauki! Ashe Abdul ya rankota!

In ta zubar da cikinsa ta shiga aukubar fushinsa tunda ya ce babu saki,in kuma ta zauna da cikin nasa kila har abada Alh ya tsere mata. Ta fara dauke kwallarta sannan ta dube shi, ta ce. "Ni bani da wani ciki abdul,har yaushe na sanka da zan yi ciki da kai... Don Allah ka saurara min ni bana son tashin hankali,in dai fita ce ba zan kuma fita ba har ranar mutuwar tawa kamar yadda ka zaba min.... ,shi ke nan? Sai dai ba zan

kasa tun mata cutar da ka yi min ta zama da ni ba tare da so rai na ba". Ta kare da kuka,amma sai ya hadiye tausayin nata da kaunar tata da ke

bijiro masa ya kawar da kai,ya ce. "Ni yanzu ta cikina da ke gare ki nake yi ba maganar fit da zaman gida ba. Fita dai ba kin riga kin yi ba,kin kuma ki sanar da ni inda kika je da abin da kika je yi, kin fita cikina yana cikin koshin lafiya,kin

dawo min da shi a wahale kina neman jaza min mummumnar asarar da ban taba irinta ba, don tsbar son Zuciya irin naku. Na rantse miki da Allahj fatima idan wani abu ya samu cikina sai na

wulakanta ki, kuma si na hada danginki na
sanar
da su abin da kika yi min..." Ta tare shi cikin
masifa. "Malam wai a ruwa zan sha cikin ne? Na
fada maka ba ni da shi...." Shi ma ya taso mata
da fada. "Ta ya ya zan gaskata bakinki da ya
saba karya? Zan gamsu kawai idan na dauke ki
na kai asibiti aka tabbar min.... Kar ki dauke ni
wani soko kin ji! Ina sa wa abin da nake so ido
fiye da yadda kike tsammanin,duk wani
motsinki
a idona yake fatima.... Saboda haka ki shiga
hankalinki". Ya mike ya kwashe kayan gabanta
ransa a bace ya fice yana ji tana rusar kuka.
Ina
mafita? Sai ta innalillahi wa'inna ilaihi raji'un
kawai, hakika tana cikin tashin hankali,Allah
ya
jarrabe ta,haka ta yi kukanta ya ishe ta,har ta
share hawayenta ta goge fuska lokacin da ta
jiyo
sallamar hindatu.ta gyara fuskar ta mike ta
fito
falon. Da walwala a fuskarta ta yi mata tayin
zama suka gaisa ta yi mata sannu da jiki,suka

dan taba hira game da ciwon fatima,ta yi mata

godiyar dawiniya har suka shihga wasu hirarakin.

Karfe sha daya dai dai sai ga laila ta same su

tare da hindatu,suka gaisa sannan ta yi musu

sallam ta fice. "Wannan 'yar makota ce?"

Fatima

ta yi dariya ta ce, "Matar mai gidan nan ce".

Laila ta zabgawa kofa harara,sannan ta karasa

ragowar akan fatima cikin kaushin murya ta ce.

"Kin bayar da mata wallahi. "Da mugun sauki

tunda ba maza na bayar ba ... Fiye mayar da

allura garmawallahi ba .. Gane wata matsalar

danne wata ta ke..." Laila ta gyara zama ta ce.

"Wani abu ya faru ne? Nan fatuma ta kwashe

mata dukkan labari tun daga ranar da suka

dawo

har zuwa jiya da yau cikin bayyana takaici da

damuwa tare da nuna kaka ni kayi,amma tana

saka aya sai laila ta saki tsaki ta dora da cewa.

"Ni fada miki tuni akwai sakacin wajen cin

kashin

da mutumin nan ke miki.... Shi din banza da

zaki

bar shi ya nemi gadar miki da hawan jini..... Don

tsabar wulakantar da kai har da wani fada

masa

ba wajen Alh kika je ba.... Ba kya barinsa ya

tafi

a haka in ya ji haushi ba sai ya sake ki ba, idan

ni ce ma ba sai na ce masa cikin ma na Alh ba

ne tunda dama shi bakarare ne.

2 · Like · React · Report · May 17, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji 2

36

A sanyaye fatima ta dakatar da ita da hannu

amma ta kasa cewa kopmai laila tabude jakarta

ta fito mata da wayarta black berry bold 2

sabuwa tana cewa. "Sai ki tashi ki shirya mu

komawa likitan ga waya inji Alh,akwai layin Glo

a

ciki " Abdullahi ya alkwartawa kansa duk

runtsin

aiki sai ya rinka saurara masa ya waiwayi

gidansa,don dora ido akan fatima.kuma daga

yau

ya fara laila ba ta jima da shigowa ba ya shigo

gidan.da hindatu ta nemi ba'asi sai ya ce mata

takardu ya manta,cikin dabara ya ce mata.

"Fatima ta fito ne?" Ba tare da ba wa

maganarsa

muhimmanci ba ta ce. "A'a Ya kuma dubanta a

nutse ya ce. "Amma dai baki ta yi ko?" Ta

gyada

masa kai,ta ce. "Eh,ta yi bakuwa kam na ganta

lokacin da na je dubo ta". Cikin bugun zuciya ya

ce. "Ko laila ce? Ta kada kai,ta ce. "Ita ce". Ya

tilasatawa kansa jarumtar hadiye rikitarsa

gaban

hindatu ya wuce yana cewa. "Ah bari na ganta".

Ya yi sallama falon,amma a ciki tsoro da razana

suka bayyana karara a fuskar fatima me rike

da

waya a hannu,wayar da gaba daya hankali da

idanuwan Abdullahi ke kanta.... Sai laila ta saki

baki tana kallon fatima wadda kamar a ce kyat!

Ta zura a guke, sannan ta juya ta kalli

Abdullahi

wanda ya dogare a bayan kujera fuskarsa babu

annuri sam! Cikin sakanin ta yi

nazarinda,kamka

ntar jikinsa bai kamata ace yana da kwarjini

ba,

amma ita kanta ya cika mata ido sai ta ji gaba

daya ya rude.ta fara gaishe shi a rikice shi

kuma

ya amsa idonsa akan fatima,ta yi saurin kawar

da

kai tana hadiye rikitarta. Ya yi kokarin

kyautata

muryarsa,cikin tsare gira ya ce. "Fatima

wannan

wayar fa? Ta dubi wayar ta dube shi, bakin ta

ya

hau rawa,ta kasa kuma fitar da sauti. Ya kara

murtuke fuska.lokacin da ya karasa gabanta ya

mika mata hannu. "Bani". Bakinrta ya hau

rawa

ta mike ta boye wayar a baya tana cewa... "Ya

ya za a yi na baka... Ni ba tawa ba ce..... Ka ga

mai ita". Ya gyara murya,ya ce. "Ai na sani ko

laifi ne don kin bani na gani....? Ta yi katfin

halin

amswa. "Ni ma ba laifi ba ne don na hana ka..."

Ya tari numfshinta cikin bacin rai. "Ban fadi

haka

don ina gudun na yi miki laifi ba, musamman da

yake zan iya murde hannunki na kwata...

Saboda

haka tun ina mutuntaki ki ba ni...." Bai ma jira

cewar tata ba ya kamo ta ya murde ya kwace wayar ya zaro ta daga kwali. Ya tarwatsata a bango ya kuma binta ya karasa sannan ya juyo gare su da ko wacce ta shiga taitayinta, ya dubi fatima da kyau.ya ce. "Wace ce wannan,me ya matsayinta a rayuwarki?" Ta yi fuska ta kawar da kai babu alamar zata tanka, sai ya rabu da ita ya fuskanci laila ya ce mata. "Bisa wace hujjar kika kawo mata wannan wayar? Duk firsarar laila sai ta kasa motsi,shi kuma ya ci gaba da yi mata kallonm uku ahu,sannan ya ce. "Ke ce wakilyar babban shaidan da karami ko? Ga shi kuma tuni na yiwa gida nan katangar karfe da shaidanu. Saboda haka duk makircin da kika kullo da abinki za ki koma,kin ga..." Ya nuna mata kofa. "Fita ki bar min gida,kar na kara ganin muguwar kafarki a cikinsa,idan ba haka ba sai na yaga miki dam mutumcin mutuntakar da ya dam fare miki... Annamimiya kawai. Fatima ta sha gabansa cikin

yanayin tashin hankali ta ce. "Abdul wane irin

cin

fuska ne wanmnan...." Ya zabga mata harara

yana nuna laila ya ce. "Wannan har tana da

fuskar da zan ci? Kin san Allah ba don

wulakanta

wulakantacce wani nau'I ne na wulakanta kai

ba

yau sai na wulakanta wannan matar.ban taba

gaini wani tsanannen mutum sama da ita ba,

sabnoda haka inda tana da fuskar da zan ci sai

na cinye tas na hutar da 'yan baya. Don haka ke

na ki saurare ni da kyau! Duk ranar da na kuma

ganinta a gidan nan taki fusakar zan ci tunda

ita

ba ta da wadda zan ci... Malama tashi ki bar min

gida na ce?" Ya kare da tsawr da ta cika gidan.

Laila ta mike cike da mugun takaici,dakin na

juyawa da ita saboda bakin ciki,fatima ta

rakota

cikin kuka tana kallon Abdullahi. "Ba zata fita

ba,sai dai in ka kore mu tare..." Ya saki wani

uban tsaki,ya ce. "Ita na kora,kuma in zaki bita

ai

ba daure ki na yi ba, iyakaci in kin bita ki ga

nawa KWANJIN.... Ba a haifi shashashar matar da zata kawo min wauta ba..." Laila ta fizge hannunta ta yi gaba tana numfashi ita kuma fatima ta kara kuka,ta ce. "Ni ce shashasha abdul?" Ya share ta ya ci gaba da bin laila da maganganu. "Idan kin je sai ki fadawa shaidanin
naki yadda na yi da ke,ki kuma tabbatar masa zai
iya nasarar raba fatima da gidan nan matukar ya
taba ganin wanda ya mutu ya farko,ki fada masa
kuma kurarin da ya yi min jiya sun bi rariya tunda
ni ba rago ne kamarsa ba..." Laila dai ko juyowa ba ta yi ba ta fice a salube,inda shi kuma ya sauke ganinsa ga fatima,ya yi tsaki ya ce. "To wace ce ke din in ba shashah ba? Ko yawan shekarunki suna miki amfani? A shashashancin ma ke ba ki shiga layin wadanda suka tara suna ba,idan kuma kina da abin yi sai ki yi.... Mts...! Aikin wofi kawai.." Yana huci ya sa kai ya fice daga falon,ai sai kawai fatima ta yi mutuwar tsaye a wajen,kuka ma ya gagara.

1 · Like · React · Report · May 17, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji 2

37Wuni ta

yi tana tanadin tashin hankalin da zata yi da

shi,

wanda zai sa shi sakinta ko da ya fi gyatumarsa

kokari,amma ina! Sai tanadinta ya tashi a

banza,

don har ta kwanta bacci bai leko inda ta ke ba

duk kuwa da cewa girkinta ne. Da safe ma tana

jinsa ya fice ya bar gidan har rana ta take,

yamma ta yi ba ta sanya shi a idonta ba,ya dawo

amma kamar yiya bai leko ta ba. Daga nan ne fa

hankalinta ya bar kan tanadin bala'inta ta

koma

na takaicin da neman mafitar yadda zata

kukuta

daga wannan tozarcin me matukar taba rai da

ya

kwaso mata a lokacin da ta ke cikin tsaka mai

wuya na bukatarsa kusa da ita,ko kuma

sallamarta ta bar masa gida tunda ya tare

tubalin

da ya rike ta a gidansa,wato kirkinsa. Ta yi kuka

ta yi abin da ya fi,amma ba ta da mai

rarrashi,ita

kuma zuciyarta ba a nutse ta ke ba bare ta nemo

mata mafita sai ma kirkiro mata wasu sababbin

koma bayan ta ke, wato kamar na janyo mata

gorin sadiya. Har ta saka kayan bacci ta kwanta

karfe goma da rabi,ta mike cikin fushi da zafin

rai

da zura hujabi ta saka takalmi ta fita zuwa

dakinsa, ko kwankwaswa ba ta yi ba murda

handle ta shiga. Yana kishingide kan sofa yana

karanta kur'ani,yana ganinta ya diga aya yayi

addu'a,sannan ya mike zaune sosai ya saka

mata ido fuskarsa babu yabo babu fallasa,ita

kuma ta yi kicin kicin da ita kamar mai shirin

sheke shi da mari. Ya mike a hankali ya isa book

case dinsa ya ajiye kur'ani sannan ya juyo cikin

dakewa ya ce mata. "Lafiya kuwa?" Ta silale a

hankali ta zauna akan hannun kujera saboda

fushi

ya sanyayar mata gabobi,kirjinta sai harbawa

ya

ke. Da ya gama fahimtarta sai shi ya saukar da

nasa fushi ya mika mata filon kujera da sauri

yana cewa. "A'a zauna sosai mana" Sai kwalla

ta

cika mata ido, ta yi saurin girgiza kai,ta ce.

"Malam ni ba zama ya kawo ni ba...." Ya sa

mata ido kawai. "Zuwa na yi na fada maka

wallahi na gaji da aurenka..... Ni dai na gaji

wallahi,kuma dole yanzu ka sake in". A sanyaye

ya ce da ita. "Me na yi kika gaji da aurena

fadima?" A kufule ta amsa masa. "Dama can a

gajiye nake,hakurina ne kawai ya kare da na

fahimci sam ba ka da tausayi.ina zaune a

gidanka bisa tilas kai kuma kana son rataye

ni...

To wallahi ba zai yiwu ba, idan ma yajin ne na

shirya in yi kuma babu mai matsa min in dawo

gidanka". Ya tuntsure da dariya ya na

dubanta,ya

ce. "Amma dai da kin ji kunya.da shekarun

talatin

da biyu ne za ki kwashi yaji gida? Yanzu laifi ne

dan na zagi zagagge? Haba fadima duk yawo da

ke da nake yi watannin kusan takwas ban gajiya

ba sai ratayar kwana biyun da na yi miki ce zata

kosar da ke? To yi hakuri na tuba ba zan kara

ba".$ ta dauke kai tana ci gaba da zubar da

hawaye. Ke nan! Su ishe ka da laifi amma ba ka

isa daukar mataki a kansu ba sai su ki da rauni da neman a basu hakuri,duk goma da ashirin! Ya tari gabanta ya ruko ta cikin murya mai bayyaya tarin kauna,ya ce. "Ki yi hakuri fadima,horo ba zai taba zama kiyayya ba, musamman a zuxiyar da ba ta da tamkar.... Matsala ta daya ce wadda sai ki min uzuri a kanta, ita ce,KAIFIN SO ba ya hana ni tsawatarwa idan an kauce hanya da zaki guji laifuka da kin tabbatar ba a cika samun masoyi kamata ba". Da muryar da ke nuna son fashewa da kuka ta ce. "Idan shashancina ya hana ni fahimtar ka fa.Ni ka karasa fice min a rai,ba ni da sauran wani abin yi a gidanka... Ni kawai tafiya..." Ya shishige mata sosai da kokarin shigar da idonsa cikin nata,ya girgiza mata kai. "A fatar bakinki wadannan kalaman suka tsaya,kafin na furta miki shashanci fadima sau nawa na furta miki kalaman yabo? Kin taba gode min ko kin mayar min da rabbi? Ki yi min uzurin

waccan kalmar na janye ta tunda ta bata miki
rai
kin ji? Na san ba zan taba fita ranki ba mun
riga
mun zama jiji da tsoka... Gidana gidanki ne ba
zaki taba barinsa ba..." Ya hanata ci gaba da
kallon tuhumar da ta ke masa ta hanyar
rungume
ta yana karadeta da sumba kawai sai ta sa masa
kuka don ta san kawai ya gama da ita. Tabbas
ta yarda ta fada taekonso wanda ko ta sami
dama zata gaza fita da kashin kanta... Wato
tarkon sonsa wanda ba ta gaskata ba sai da
rikice rikicen nan nasu suka bullo,idan ya yi
fushi
sai jininta ya nemi hawa.da ya kaurace mata
jiya
da yau sai zuciyarta ta nemi bugawa,yanzu ta zo
ta tuhume shi ya cika mata ido har dadin bakin
da yake mata sun samun muhalli a zuciyarta.da
ya rungume ta sai zuciyarta ta warware kullaci
ta
sami aminci ta ji kamar dukkan matsalarta ta
duniya ta warware. Ta fara kokarin kwacewa
daga gare shi,sai ya yi dabarar zare makullai

din

hannunta ya tura aljihu, sannan ya ja ta

kujera ya

zauanar yana cewa. "Ki yi hakuri fadima!'Yan

kwanakin nan sai bata miki rai nake ko? Ki yi

hakuri aski ne idan ya zo gaban goshi ya fi

zafi...

Bari na kawo miki ruwan sanyi ki sha. Ya wuce

ba ta . Da ya ji ta bakinta ba. Ta bi shi da kallo

tana shakkar halin da ta tsinci kanta

tsakaninta

da shi. Haka ya dinga janta da maganganu na

nuna kauna da sanyaya rai, yana ba ta labaran

ban dariya, amma ta ki sakewa damtse ya kawo

musu abinci ya yaudare ta suka ci tare yana

labarta mata rabonsa da cin abincin kirki,tun

shekaran jiya. Ko a ranta ba ta karyata shi ba

don ta ga alamar rama a fuskarsa. Ta dubi

agogon da ya nuna sha biyu da kwata, sai ta

fara

neman makullanta ya yi dariya ya ce. "Na

adana

miki su,ai na yi tsammanin za ki taya ni kwanan

a nan". Sai ta kasa musa masa, shi kuma ya ci

gaba da himmar dauke damuwa daga

zuciyarta,har ya sami rage kaso mai tsoka.musamman da ya ke ya share ta da maganar ciki,kuma hakan ne ya sa ta nutsuwar rai,ta yi bacci har da saleba a kirjinsa. Yaya da ta

barshi da tunanin shaukin nasarar da ya samu a kanta.tabbas saura kiri ya gama mallakar zuciyarya,zuciyar da babu wani kaunarsa da ya raba samunta. Ranar bai runtsa ba, don sai sulu sin daren bacci ya rika fizgarsa,amma ya daure masa ya tashi ya gurfana gaban mahalicin shi khushu'I dauke tarin bukatunsa. Sai bayan ya dawo masallacin suka hau rama baccin tare son dama gaba dayansu sun ci bashinsa,kwana biyu,Allah kuma ya yi musu gamon katar week end na,ba su tashi ba sai sha daya ta haura. Haka suka wani yana lallabarta tare da nuna mata kauna,ya share maganar cikin tsab! To ita ma duk da ba ta ba shi raddi to ba ta gwale shi ko kuma turbune masa fuska,sai ya zamana ya sami kansa da farin cikin da bai taba samu daga gare ta ba, tunda ya aureta. Da yamma ya lalaba

ta suka fita da zummar ya kai ta su gayar da kawu da momi,kuma ya kirkiro fitar ne don ya

faranta mata,sai daiba ta yi farin cikin ba,don

ba

ta kaunar su ganta da ciki har su fara yamadidi

da ita a dangi zancen ya fito Alh ya zatar mata

cin amana.Amma babu yadda ta iya tunda abin

kunya ne ta nuna masa ba ta son zuwa

danginta,sai ta yi shahada ta bi shi suka tafi.

Me

zai faru? Karbar da suka yi mata ta kada mata

ciki kwarai,har ta fara zargin ko dai Abdullahi

ya

tona mata asirri ne? Kallon arziki ba ta samu

daga kawu ba, gasuwar tata ma ciki ya

amsa,dukkan kulawarsa da fara'arsa tana ga

Abdul,momi kuma sai wani irin kallo ta ke

mata,don haka a tsorace ta bar musu wajen ta

tafi wajen su safiyya. Babu jimawa momi ta aiko

akayi kiranta,ta same ta dakinta.ta nemi gurin

zama tana satar kallonm idon momi,wadda sam

babu annuri a ciki. "Me ne ne matsayi laila a

wajenki da kika yarda ta fi mu sonki,ta fi

mijinki

sonki,sannan ta fi mu sanin dukkan abinb da

zai

amfane ki? Tambayar da momi ta jefo mata ke

nan cikin kaushin murya wadda sai da ta janyo

cikinta ya juya.

1 · Like · React · Report · May 17, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji 2

38

Saboda firgita don haka ta kasa ko motsi bare ta

amsa sai da momi ta kara daure fuska ta ce.

"Ko

ba kya ji?" Ta muskuta ta kwaso in'ina da

rashin

ma'anar zance. "Wallahi... Wal... Momi

kururuta

lamari ne kawai irin na Abdul..... Ba ki ga cin

kashin da ya yi mata ba rannan.... Wai kar ta

kara zuwar masa gida.... Ni ban ga laifin da ta yi

ba....' Momi ta bude ido da kyau tana kallonta

cike da takaici,ta ce. "Kin ga kin kara bayar da

shaida a kanta da kuma abin da kanwar uwar

Alh

ta zo mana da shi gidan nan,don kwata kwata

babu Abdullahi cikin wannan maganar,tsoro na

daya Allah ya sa bai san da maganar kin kai wa

likita cikinsa ya cire ba... Haka ne? A kalolin

tashin hankali babu wanda bai birkito a zuciyar

fatima ba, yanzu ta fahimci lamarin babba

ne,sai

kawai ta yi zuru numfashinta na bugawa dai

dai.

Momi ta koro bayani cikin bacin rai. "Jiya har

kusan iyanzu Haj sa'adatu kanwar uwar Alh

tana

nan tana zuba mana tijara iri iri da kashe

kashede

saboda yunkurin kashe aurenki da kike don ki

koma gidan dansu,wai har da yunkurin zubar da

ciki... Fatima wacce irin busa duniyar na ke yi

miki? Da kin mutu wajen wannan yunkurin naki

me za ki fada wa Ubangijiki...? Fatima ta dade

kirji cikin tsoro da tashin hankali ba na batun ta

zubar da ciki ba, na ta inda maganar ta fita har

ta isa kunnen dangin Alh. A rikice ta ce. "Momi

inji wane gwanin sharrin? Ni ina ma na ga cikin

da har zan zubar?" Momi ta yi mata wani

mugun

kallo ta ce. "Ko? To wa kike da shi wanda ya

wuce kawarki laila? Idan sharrin ne ma ita ta yi

miki don ta tabbatar da ita kuka je asibitin....

To

ko sharri ne dai ni da kawunki mun gaskata don

mun san za ki aikata,ke fa tuni mun fahimci
yunkurin kashe auren da kike daga inda
Abdullahi
ya hana ki waya ya hana ki mota,ya hana ki
kula
da sauran kasuwanci ki muka san akwai wata
akas. To karkade kunnenke da kyau,daga cikin
kalaman cin mutunci da sa'a ta yi mana ta
furta
cewa,idan ma zafin talauci ya fara ratsa ki kike
son komawa gidan dansu,to ki yi magana za su
dinga yankar miki wasu kudade masu kauri duk
wata, su dai ba sa kaunar zamakin cikin a
halinsu
don ke ba alkhairi ba ce a rayuwar dansu. Sai
kuma sakon prof.ya tabbatar miki in sanar miki
daga inda kika kaso aurenki shi kuma wallahi ya
sallame ki,sai dai ki nemi wani uban ba shi ba. Ni
ma kuma na goya masa baya fatima,ki nemi
wata
uwar ba ni ba, Allah ya gani mun yi iyakar namu
kokari har fitinarki ta gajiyar da mu.... To bai
kamata a yi mutuwar kasko ba, ke kin sarayar da
naki mutuncin da kimar,mu kuma mu yarda mu
sarayar da namu ta dalilinki ba... Ina amfanin

wulakancin da sa'a ta zo ta yi mana jiya?"

Kawai

sai momi ta fara hawaye. "Innalillahi wa inna

ilaihi raju'un" kawai fatima ke maimaitawa a

cikin

ranta lokacin da ta ji. Zuciyarta ta yi nbala'in

kuntato,tsoro,b acin rai da bakin cikin sun cika

ta

tafi ita ma sai hawaye ta ke ta kasa tankawa.

Sai da ta ga momi ta mike zata bar mata falon

sannan ta yi saurin ruko ta ta fara fitar da

sautin

kuka mai tsuma rai. "Momi ku yarda da ni akwai

sharri cikin maganar nan...." Momi ta tare ta a

kufule. "Ai daga maganarki ta farko kika

kankare

sharrin don me? Ko daya babu Abdullahi cikin

maganar nan, amma ina fara magana kika

kokar

kare,babu dalili zai kore ta? Ko kiransa zan yu

na

ji daha gare shi?" Da sauri ta girgizxa kai cikin

kuka,momi ta yi tsaki ta dora. "Sannan kin ce

ina

ma kika ga cikin da za ki zubar, wannan na

jikinki

me ye? Ko don kin tanadar masa zubewar kike

nufin za ki iya nunke mu bai bai? To me kike

shakka ne bayan ke kika haifi kanki? Ai kawai ki

yi dukkan abin da ranki ya. Kawata miki, mu

mun

zama 'yan gani da ido a cikin rayuwarki" Ba ta

jira cewarta ba ta yi tafiyarta ta barta tana

cikin

matsananciyar damuwa don haka ya kyale ta

tayi

tunani a nutse har zuwa gabar da zai sami abin

ce mata. Duk da dare ne hasken fililun titi da

na

motoci suka sanya shi gane motar da ke

gabansa, wato ta Alhaji ce direba na jan Alh da

kuma wata mace. Ya juya ya dubi fatima,sai ya

lura hankalinta ba ya jikinta,ta rafka taguni

kawai

fuskarta da alamun hawaye. Ya ciji lebe cikin

murmushi keta,ya ce. "Fadima kin gane motar

nan da ke gabanmu?" A sanyaye ta dago ta

kalli

gabanta, kallo daya ta gane abin da ke

faruwa,sai

kawai ta kawar da kai da sauri,Abdullahi ya sauke numfashi yana kallonta a kaikaice,ya ce. "Dama ya yi aure ne?" Ta yi dif har ya gaji da kallonta ya mayar da kai zuwa titi, har lokacin da

motar alh ta saka siginal zata shiga wani gida kayan sanyi,kawai sai abdullahi shi ma ya sanya siginal ya take masa baya. Da sauri fatima ta dube shi bakinta na rawa amma ta kasa magana.

Ba tare da ya dube ta ba,ya ce. "Waccan matar ce ta yi min kama da laila, Shi ne nake so in tabbatar". Ambaton sunan laila kawai wani katon

rauni ne a zuciyar fatima bare batun wai ga ta tare da Alh,da kuma wannan daren, sai ta ji numfashinta ya fara sasarfa tana bin motar da kallo har ta yi fakin,su na ma suka yi fakik nesa da su. Direba ya fito ya bude wa Alh,sannan laila

suka fito suka shiga ciki tare. Abdullahi ya dauke

kai yana kada kai hade da rera wakar cin amanar

kauna,fatima ta yi dif saboda zuciyarta ta kara

wani zafi,ji ta ke ina ma yanzu ta hadiye
zuciyar
ta bar duniyar gaba daya, wanne irin tashin
hankali ta ke tsintar kanta a ciki yau? Sai da
abdullahi ya koshi da yarfeb da yake
mata,sannan
ya yaficeta ya balle murfin motar yana cewa
"Zo
mu shiga mu ga abin da suke yo don kar mu
yanke musu hukunci da zato". Kawai sai ta sami
kanta da zuciyar balle murfin motar ta fito ta
bi
shi suka jera. Alh da laila an kama kujera ana
ta
kurbar fresh milk cikin annashuwa, Abdullahi ya
zarce karbo musu na su kason,amma fatima
idonta rufe ta nufi wajen su kai tsaye. Alh na
dora
ido a kanta zumbur sai ga shi a tsaye cikin
tsnannin rikita,da ambaton. "Fatima! Ya ya
aka yi
kika san ina nan? Cikin tsananin fushi ta ce.
"Ba
kai na biyu ba, wannan muna fukar na shigo in
gani da idona.." A dan kunyace laila ta ce. "Da

na

yi miki me? Don kin ganmu a nan tare? Ai

matsalarki muka zo tattaunawa a sirri". A

tunzure

fatima ta ce. " Ai ni ba ni da matsla wallahi,ke

da

shi ku. Ne masu matsala don ba ku ganni ina

ketare gwadabe na ba..." Alh ya yi dira dira

cikin

rudewa,ya yi kamar zai ruko hannunta, ta yi

saurin ja da baya. Dai dai lokacin Abdullahi ya

iso

da ice cream a hannunsa na dama yana

sha,yana

kuma rike da wani a hannunsa na hagu,da

alamin

ko a jikinsa hayaninyar da ya tarar.ya mikawa

fatima daya ice cream din yana cewa. "Ashe

abokin arziki kika hango kik barni ni kadai? Ta

runtse ido alamun tsanarsa bacin rai ta bude

idop

tana duban ice cream din da yake nuna

mata,ta

ce. "Abdul ba zan sha ba. Sai kawai ya ja

kujerar

ya zauna yana lasar ice cream dinsa,ya ce. "To ku gama gaisawa mu tafi" Nan fa alh ya zo wuya,cikin shakewar numfashi ya ce. "Abdullahi har ka kai tsawon da zaka yi min wannan cin mutuncin,ka san kuwa ba ka isa ba? Me ya hado ka fita da fatima....? Karaf cikin masifa fatima ta tari numfashinsa. "Kai da girmanka me ya hadoka fita da wannan tsinanniyar?" A rikice Alh ya zaro ido,ya ce. "Fatima goyon bayansa za ki yi, kina nufin abdullahi ya fi ni matsayin a wajenki...? Fatima kin san kuwa muhimmancin ki a rayuwata...? Na rantse miki zan iya komai don na tsira da ke, ciki kuwa har da kisan kai idan ta kama... Saboda haka kai ka shiga taitayinka". Yasa kai ya fice a fusace. Fatima ta janyo wani dogon tsaki ta dauke kai kai daga kallonsa ta sauke akan laila wadda ta yunkuro ta ke son ta wanke kanta. "Fatima ni kike kira tsannainya...?

"To me ce ce ke? Mijin aurenki ne ya kwaso ki a bayan mota kuka nufo nan don ku sha minti, da

wannan daren ko? Kawance da ke ai bai yi ba laila..." Ita ma laila ta zo wuya don haka ita ma ta yunkuro cike da bacin rai. "Ai babu bambanci tsakanina da ke, shi wannan matsiyacin da kika dauko kuka taho nan me ye a tsakaninki da shi...?

Like · React · Report · May 17, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji 2

39

Fatima ta tare ta. "Akwai abin da tsinancewar ki

ta hana ki taka matsayinsa,wato aure,kin san kuwa ko banza masa ta fi kashin shanu,don ko me wankin takalminsa kika samu ya adana ki a dakinsa ya fi wannan gantalin da kike... Ko da yake ina tsammanin kin yi zaton gulama da sharrinki ya ishe ki taka matakan da na taka, kika

kwashi kafa dangin Alh tsugudidi..." Jin fatima ta

debo fasa mata ciki ya sanya ta tarewa da nufin tona mata asirin gaban mijin da ta ke shakka. "Auren naki na gaibu,mara ma'ana da manufa...

Ai in dai bariki ne, to tare muka kwaso shi da ke,ko kin taba ni zuba da ciki? Ni kuwa satin da ya wuce ma na raka ki zubar da ciki,a uare kika sami cikin kika zubar?" Sai a lokacin fatima ta tuno akwai Abdullahi a wajen.ta yi saurin dubarsa

cikin tsoro da firgici amam sai ya dauke kai,fuskarsa kuma ba ta fassara mata komai ba,ya koma bin laila da kallo wadda ta ke ficewa daga wajen. Fatima ta yi tsaye kawai a wajen cikin yanayi na kila wa kalan yadda rayuwa zata cinmata. Abdullahi ya dake ya karasa shan ice cream dinsa ba tare da ya dubeta ba,ya ce. "Zo mu tafi" Inna lillahi wa innan ilaihi raju'un,ta ambata a ranta ta sa kafa ta biyo shi cike da fargabar ruwan bala'in da zai sheka mata idan sun koma gida,ko kuma kalar fushin da zai mata

wanda ta tabbatar wanna dole ne daga yadda ta

fahimci takunsa a yanzu. Bai ko jira ta sun jera ba ya wuce mota,ita kuma ta bi shi kamar kazar da kwai ya fashewa a ciki, ya shige mota abinsa ba tare da ya bude mata kamar yadda ya saba ba. Jikinta na bari ta bude ta shiga ya tashi

motar ya fice a fusace. Suna fitowa daga

harabar

wajen suka wuce laila tsaye tana ta faman tare

adai daita sahu,suna wucewa saboda daren da

ya

fara yi. Har sun dan gota ta kadan sai Abdullahi

ya sauka titi a hankali,ya yi fakin bai tankawa

fatima ba ya fice daga motar.ta bi shi da kallo

cikin dukan zuciya,sai ta ganshi kai tsaye laila

ya

nufa. Nan numfashinta ya fara yin sama

sakamakon hargitsawa da cikinta ya yi,ciwon

cikinta ya dawo mata sabo. Duk da haka ba ta

kasa dauriyar tattara hankalinta ka su ba.

Kafin

ya karasa laila ta fara tafiya,don haka yana

tarar

da ita suka jera. A nan zan dakata sai mun

hadu

a littafi na uku taku..... Amierah S man meh copy n paste. ....

Compelled by hauwee jidderh abdulkadir AKA mss jidderh